# Sharhin Usulul imani

**[Hausa]**

**Sheikh: Muhammad Bin Saleh Al'usaimin.**

***Fassarar: Ibrahim Abdullahi Abubakar***

***Dubawar: Aliyu Muhammad Sadisu***

# شرح أصول الإيمان

(الهوسا)

## الشيخ محمد بن صالح العثيمين

ترجمة: إبراهيم عبد الله أبوبكر

مراجعة: علي محمد سادس

# Gabatarwar wanda ya duba

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, tsira da amincin Allah su kara tabbata ga Annabinsa Muhammad ﷺ da iyalansa da kuma sahabbansa baki daya.

Bayan haka; Wannan fassarara ta wannan littafi mai matukar muhimmanci da ya kunshi takaitaccan bayani akan abinda ya shafi shika-shikan Imani, falalarsu alkhairansu da kuma matsayin musulunci ga wadanda ba su yi Imani da su ba. Littafin ya share fage da bayanin tsaftatacciyar akidar musulunci, sannan sai ya koro bayanai akan Usulul Imani wato shika-shikan Imani, kana kuma littafin bayan haka sai

ya rufe da bayani akan manufofin akidar musulunci.

Wannan littafi mai suna ***"Sharhin Usulul Iman"*** ya zo a daidai lokacin da ake matukar bukatarsa, kuma ga shi Shehin malamin ya yi bayani gamsasshe kuma takaitace, sannan shi kuma dan'uwa malam Ibrahim Abdullahi ya fassara shi zuwa harshen Hausa, lalle wannan ba karamin aiki ba ne, Allah madaukakin sarki ya saka musu da alheri baki dayansu.

**Wanda ya duba:**

*Aliyu Muhammad Sadisu,*

*Minna,*

*Nigeria.*

*email:aliyusadis@gmail.com*

## Da Sunan Allah Mai Rahma, Mai Jin Kai.

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah, muna yaba masa, kum muna neman taimakon sa, muna neman gafaransa, muna tuba a gareshi, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrin kawunan mu da kuma munannan ayyukan mu. Duk wanda Allah ya shiryar babu mai badar da shi, kuma duk wanda ya batar to babu mai shiryar da shi. Ina shaidawa babu abin bauta da cancanta sai Allah, shi kadai yake ba shi da abonkin tarayya, kuma ina shaidawa lalle Annabi Muhammad (ﷺ) bawan sa ne kuma manzon sa ne tsira, da amincin Allah su tabbata a gare shi da iyalensa da sahabban Sa da

kuma wadanda suka bi su da kyautatawa aminci ya tabbata a garesu.

Bayan haka, lalle ilimin Tauhidi yana daga cikin manyan ilimi, kuma wanda yake da girman daraja, wanda ya zama wajibi a nema, domin shi ne ilimin sanin Allah ta’ala da sunayensa da siffofin sa da kuma hakkokin sa akan bayin sa.

Domin shi ne mabudin hanyar saduwa da Allah ta’ala, kuma gimshirkin shari’ar sa. Da haka manzannin Allah suka taru domin kira zuwa gareshi Allah ta’ala ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥﴾ الأنبياء: ٢٥

**Ma'ana:** *"Kuma bamu aika da wani Manzo kafinka ba face mun masa wahayi cewa babu wani abun bauta sai ni"*. (Al'Anbiya'i, aya ta:25).

Allah shi da kansa ya tabbatar da kadaitakarsa, haka malaiku suma sun shaida da ma'abota ilimi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلۡعِلۡمِ قَآئِمَۢا بِٱلۡقِسۡطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٨ ﴾ آل عمران: ١٨

**Ma'ana:** *"Allah ya shaida lalle shi babu wani abun bauta da da cancanta sai shi, malaiku ma sun shaida da ma'abota ilimi tsaye suke da adalci akan haka, babu wani abun bauta da da cancanta sai shi, babu wani abun*

*bauta sai shi mabuwayi mai hikima”*. (Suratu Ali Imaran, aya ta: 18).

Game da tauhidi, abune wanda ya kasance dole a koya kuma a koyar, a lura kuma a kudurce a zuciya, don a gina addini akan tubali ingantacce da natsuwa, da mika wuya zuwa ga abin da zai samar da kyakkyawan sakamako.

**ADDININ MUSULUNCI.**

Addinin musulunci shi ne addinin da aka aiko Annabi Muhammad (ﷺ) da shi, kuma da shi ne Allah madaukakin sarki ya cika addini da Ibada, kuma ya cika na'imomin sa a garesu, kuma ya yardar musu da zama addini, ba za'a karbi wani addini ba sai shi, Allah ta'ala ya ce:

﴿ مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمۡ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ﴾الأحزاب: ٤٠

**Ma'ana:** *"(Annabi) Muhammad bai kasance uba na daya daga cikin mazajanku ba sai dai Manzon Allah ne kuma cikomakon Annabawa"*. Suratul Ahzab, aya ta:40.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗا﴾ المائدة: ٣

**Ma'ana:** *"A yau ne na cika muku addinin ku, kuma na cika muku ni'imata kuma na yardarm maku addinin ku, kuma na yardar muku addinin musulunci shi ne addini"*. Suratul Ma'idah, aya ta: 3.

Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُ﴾ آل عمران: ١٩

**Ma'ana:** *"Karbabban addini a wurin Allah shi ne musulunci"*. Suratu Ali Imrana, aya ta: 19. Allah ya ce:

﴿ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥ ﴾ آل عمران: ٨٥

**Ma'ana:** *"Duk wanda ya riki wani addini wanda ba musulunci ba to ba za'a taba karba daga wurin sa ba, kuma shi a lahira yana daga cikin asararru"*. Suratu Ali Imrana, aya ta:85.

Hakika Allah ya farlanta akan dukkan mutane da su yi addini kadai ga Allah, ya fadi haka yana Magana da Manzon Sa (ﷺ):

﴿ قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُمۡ جَمِيعًا ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ

وَرَسُولِهِ ٱلنَّبِيِّ ٱلۡأُمِّيِّ ٱلَّذِي يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَكَلِمَٰتِهِۦ وَٱتَّبِعُوهُ لَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ١٥٨ ﴾ الأعراف: ١٥٨

**Ma'ana:** *"Ka ce ya ku mutane lalle ni manzon Allah ne zuwa gare ku baki-daya wannan da yake da mulkin sammai da kassai, babu abun bautawa cancanta sai shi, mai rayarwa mai kashewa, saboda haka ku yi imani da Allah da ManzonSa Annabi Ummiyi wanda ya yi imani da Allah da kalmominSa, kuma ku bi shi domin za ku zama shiryayyu*. Suratul A'araf, aya ta: 158.

Kuma a cikin sahihi Muslim daga Abi Huraira Allah ya yarda da shi, daga Manzon Allah tsira da aminci Allah su tabbata a gare

shi ya ce: *“Ina rantsuwa da wanda rayuwar (Annabi) Muhammad take a hannunSa babu wani da zai ji sako na daga cikin wadannan al’ummar Bayahude Ko Banasare (Kirista) sannan ya mutu bai yi imani da abun da aka aiko ni da shi ba face ya kasance daga cikin ‘yan wuta”*.

Kuma imani da shi (ﷺ): Shi ne gasgata duk abun da yazo dashi tare da karba da kuma da kuma aiki da shi, ba kawai gasgantawa ba kadai, da haka ne Abu-Talib bai yi imani da Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi)ba, tare gasganta abun da ya zo da shi, kuma bada shaida da cewa shi ne mafi kyawun addini.

Addinin Musulunci ya kunshi dukkan maslaha da addinin da suka gabata suka kunsa, yana da banbanci da su, domin kasancewar sa ya yi daidai da kowannne zamani, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَمُهَيْمِنًا عَلَيْهِ ﴾المائدة: ٤٨

**Ma'ana:** *"Kuma mun saukar da littafi a gareka da gaskiya, mai gasganta abin da ke gaba gare shi na littafi kuma mai hukunci a gare shi"*. Suratul Ma'idah, aya ta:48.

Ma'anar kasancewar ya yi daidai da dukkan zamani da kowacce kasa da kuma kowacce al'umma: Lalle riko da shi ba ya kore

kyawawan manufofin al’umma a kowanne zamani da kuma kowacce kasa, sai dai gyara kawai, ba wai abinda mutane suke cewa ba ne wai yana tawaye mutane a kowannne lokaci da kasa da kuma ci-gaban al’umma kamar yadda mutane ke nufi.

Addinin musulunci shi ne addinin gaskiya, wanda Allah ya yi alkawarin taimaka wa wanda ya yi riko da shi matukar riko, kuma zai daukaka shi akan wanin sa. Allah ta’ala ya ce:

﴿ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِينِ ٱلۡحَقِّ لِيُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡمُشۡرِكُونَ ٣٣ ﴾ التوبة: ٣٣

**Ma'ana:** *"Shi ne wannan da ya aiko da Mazon Sa da shiriya da kuma addini na gaskiya domin ya daukaka shi akan sauran addini ko da mushirikai sun ki"*. Suratut Tauba, aya ta: 33.

﴿ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَيَسۡتَخۡلِفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ كَمَا ٱسۡتَخۡلَفَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ وَلَيُمَكِّنَنَّ لَهُمۡ دِينَهُمُ ٱلَّذِي ٱرۡتَضَىٰ لَهُمۡ وَلَيُبَدِّلَنَّهُم مِّنۢ بَعۡدِ خَوۡفِهِمۡ أَمۡنٗاۚ يَعۡبُدُونَنِي لَا يُشۡرِكُونَ بِي شَيۡـٔٗاۚ وَمَن كَفَرَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٥٥ ﴾ النور: ٥٥

Allah ta'ala ya ce:

**Ma'ana:** *"Allah ya yi alkawari ga wadannan da suka yi imani daga cikin ku, kuma suka yi aiki nagari wallahi za mu halifantar da su a*

*bayan kasa kamar yadda muka halifantar da wadanda suka kasance a gabanin su, kuma ya tabbatar da su a cikin addinin da ya yardarm musu, ya kuma canza musu tsoro ya kawo musu zaman lafiya, suna masu banta mini ba sa hadani da kowa, kuma dukkan wadanda suka kafirce bayan haka to wadannan sune fasikai".* Suratun Nur, aya ta: 55.

Kuma addinin musulunci: Imani ne da kuma hukunce-hukunce, kuma cikakkene a imanin sa da kuma sheri'arsa.

1. Yana umurni da tauhidi kuma yana hami da shirka.

2. Yana umurni da gaskiya kuma yana hani da karya.

3. Yana umurni da addalci kuma yana hani da zalunci.

4. Yana umurni da amana kuma yana hani da ha'inci.

5. Yana umurni da cika alkawari kuma yana hani da rashin sa.

6. Yana umurni da biyayya ga iyaye kuma yana hani da butulcewa iyaye.

7. Yana umurni da sada zumunci ga 'yan-uwa kuma yana hana yanke zumunci.

8. Yana umurni da kyautatawa makwafta kuma yana hani da munana masu.

Gamamiyar Magana anan ita ce, shi musulunci yana umurni da dukkan kyakyawa ma'amala kuma yana hani da dukkan abinda yake kishiyar haka.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُ بِٱلۡعَدۡلِ وَٱلۡإِحۡسَٰنِ وَإِيتَآيِٕ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَيَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡبَغۡيِۚ يَعِظُكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ٩٠ ﴾ النحل: ٩٠

**Ma'ana:** *"Lalle ne Allah yana umarni da adalci da kuma kyautatawa da kuma bayarwa ga makusanta, Kuma yana hana alfasha da munanan ayyuka da zalinci,*

*(Allah) yana muku wa'azi domin za ku zama masu daukar tunatarwa"*. Suratun Nahli, aya ta: 90.

# RUKUNAN MUSULUNCI.

Rukunan musulunci su ne wadannan da musulunci ya ginu a kai, su ne kuma guda biyar wadanda zamu ambata a cikin hadisin Abullahi dan Umar Allah ya yarda da su daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce:

"An gina musulunci akan abubuwan biyar: Akan su kadaita Allah (a wata riwaya kuma): Shaidawa babu abun bautawa da cancanta sai Allah kuma Annabi Muhammad bawansane kuma ManzonSa, da tsaida sallah, da bada zakkah, da azumtar watan Ramadan da Hajj". Sai wani ya ce: Hajji da

Azumin Ramadan’. Sai ya ce: “A’a, Azumin Ramadan da Hajji. Ita na ji daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi (Bukhari da Muslim). Amma lafazin muslim ne.

1. Amma Shidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma lalle Annabi Muhammad (ﷺ) Manzon Allah ne, kuma bawan sa ne. Shi ne kudurice wa ta hakika wadda harshe ya furta da wannan shaidawar, kamar ka ce yana ganin wanda ya shaidashi. Kuma a sanya wannan ta zama rukuni daya ne tare da cewa wanda aka shaida da shi din Allah ne da Manzonsa.

Amma shi Manzon Allah mai isarwa ne game da sakon Allah ta'ala, shaidawa da shi a matsayin sa na bawa kuma manzao, yana cikon shaidawa da Allah a matsayin abin bauta.

Amma wadannan shahada biyu tushe ne na kyautatuwar ayyuka da kuma karban su, domin babu karbuwa ga duk aikin da babu tsarkake Allah a cikin sa, tare da biyayya ga Manzon Allah (ﷺ) tare da iklasi ga Allah ne shahada ke tabbata, haka ma tare da bin Annabi (ﷺ) shahada ga Annabi take tabbata.

Daga cikin manyan abuwan da mutum zai more idan ya yi kalmar shahada sune; Haramta wa zuciya bauta wa hallitun Allah

da kuma barin bin wani wanda ba Manzon Allah (ﷺ) ba.

1. Tsaida sallah: shi ne bautawa Allah tare da aikatata ta fuskar tsayiwa da kuma cikata akan lokacinta da kuma yaddk aka koyar da ita.

Daga cikin falalar ta akawai: Bude zuciya, da samun natsuwa da kuma kariya daga alfahsha da munanan ayyuka.

2. Amma bada zakka shi ne bautawa Allah ta hanyar bada gwargadon abin zakka ta wajaba a kan shi na dukiyar da ake fitarwa da zakkah.

3. Daga cikin falalar ta, akwai tsarkake zuciya daga rowa da kuma toshe bukatuwan musulmi da musulunci.

4. Amma azumin Ramadan shi ne; Bauta wa Allah ta hanyar kamewa daga barin cin abinci ko abin sha a yinin Ramadan.

Daga cikin falalarsa akwai; ladabtar da zukata wajan barin abin da take so domin neman yardar Allah.

5. Amma ziyarta dakin Allah shi ne bautawa Allah da nufin ziyarta daki mai alfarma domin tabbatar da shari’ar Allah.

Daga cikin falalarsa, akwai ladabtar da zuciya akan kokarin amfani da dukiya da jiki

wajan biyayya ga Allah, da haka ne Hajji ya kasance bangare ne na jihadi saboda Allah.

Wadannan falala duk da muka ambata da wadanda ma ba'a ambatosu ba suna sa al'ummar musulmi tsarkake addinin su ga Allah don yin addinin gaskiya, tare da mu'ammalantar 'yan-uwa ta hanyar gaskiya da adalci, domin kuwa duk sauran shari'ar musulunci suna kyautatuwa ne da wadannan ginshikan ta kuma gyara rayuwar al'umma tare da gyara lamuran addinin ta.

Dukkan wanda ke son cikakken bayani sai ya karanta fadin Allah madaukakin sarki:

﴿ وَلَوۡ أَنَّ أَهۡلَ ٱلۡقُرَىٰٓ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ لَفَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَرَكَٰتٖ مِّنَ
ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَٰكِن كَذَّبُواْ فَأَخَذۡنَٰهُم بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٩٦
أَفَأَمِنَ أَهۡلُ ٱلۡقُرَىٰٓ أَن يَأۡتِيَهُم بَأۡسُنَا بَيَٰتٗا وَهُمۡ نَآئِمُونَ ٩٧ أَوَأَمِنَ
أَهۡلُ ٱلۡقُرَىٰٓ أَن يَأۡتِيَهُم بَأۡسُنَا ضُحٗى وَهُمۡ يَلۡعَبُونَ ٩٨ أَفَأَمِنُواْ
مَكۡرَ ٱللَّهِۚ فَلَا يَأۡمَنُ مَكۡرَ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡقَوۡمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٩٩ ﴾
الأعراف: ٩٦ - ٩٩

**Ma'ana:** *"Da mutanen birane za su yi imani kuma su ji tsoron Allah wallahi zamu bude musu kofofin albarka daga sama da kasa, sai dai sun karyata sai muka kama su da abin da suka aikata. Shin mutanen birane sun aminta cewa azabar mu ta zo musu ne daddare a lokacin suna bacci?. Ko kuma mutanan birane sun aminta azabar mu ta zo musu da hantsi a lokacin suna wasa?. Shin*

*sun amintane da azabar Allah?, to babu mai amincewa azabar Allah sai mutanan da suke asararru”*. Suratul A’araf, aya ta: 96-99.

Kuma ya dubi tarihin wadanda suka gabata, domin a cikin tarihin akwai abin lura ga mutane masu hankali da basira da mutunci da bai sanya wa zuciyar sa bukatun duniya ba. (Allah ya taimakemu).

# GIMSHIKAN AKIDAR MUSULUNCI.

Addinin musulunci kamar yadda bayani ya gabata; “Akida ce da kuma Shari’ah”, hakika mun yi nuni zuwa ga wasu abubuwa daga Shari’ar sa kuma mun ambato rukunansa wadanda idan an kura sune ginshikan musulunci.

Amma akidar musulunci abin da yake ginshikin ta shi ne; Imani da Allah, da Mala’iku da Littattafai da Manzanni da Ranar karshe da kuma Kaddar alheri ko sharri.

Hakika Allah ya yi nuni da su a littafinsa kuma Annabi (ﷺ) ya fada a cikin hadisan Sa. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ ۞ لَّيْسَ ٱلْبِرَّ أَن تُوَلُّوا۟ وُجُوهَكُمْ قِبَلَ ٱلْمَشْرِقِ وَٱلْمَغْرِبِ وَلَٰكِنَّ ٱلْبِرَّ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلْكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّۦنَ ﴾ البقرة: ١٧٧

**Ma'ana:** *"Ba shi ne biyayya kadai ba ku jujjuya fuskokinn ku ga mahudan rana da mafadarta, amma abinda yake shi ne addini duk wanda ya yi imani da Allah da ranar karshe da mala'iku da ittafi da annabawa"*. Suratul Bakara, aya ta:177.

Kuma Allah madaukakin sarki ya fada game da kaddara, ya ce:

﴿ إِنَّا كُلَّ شَيْءٍ خَلَقْنَٰهُ بِقَدَرٍ ۝٤٩ وَمَآ أَمْرُنَآ إِلَّا وَٰحِدَةٌ كَلَمْحٍۭ بِٱلْبَصَرِ ۝٥٠ ﴾ القمر: ٤٩ - ٥٠

**Ma'ana:** *"Hakika mun halici kowanne abu da kaddara. kuma lamarin mu bai zamo komai ba saidai kamar keftawar ido ne"*. Suratul Kamar, aya ta:49-50.

Daga cikin Sunnah (Hadisi) Annabi (ﷺ) yana cewa: Lokacin da ya amsa wa mala'ika Jibrilu (عليه السلام) tambayarsa game da imani sai ya ce:

*"Immi shi ne; Ka yi immi da Allah da malaiku da littattafai da Manzanni da ranar karshe kuma ka yi immi da kaddarar alheri ce ko ta sharri"*. Muslim ya ruwaito shi.

**IMANI DA ALLAH.**

Imani da Allah ya kunshi lamura huda:

1. Imani da Samuwar Allah.

Hakika dabi'a (fitra) da hankali da shari'ah da gababuwan jiki sun tabbatar da akwai Allah.

(a) Amma dalili game da dabi'a akan samuwar Sa; Lalle kowacce hallita an halicce ta ne da dabi'a ta imani, an yi halittar sa ba tare da sai ya yi tunanin abin da ya gabata ko ya koya ba. Babu mai canjin wannan sai wanda ya sanya wa kansa abin da ke iya sanya shi. Annabi (ﷺ) ya ce: *"Babu wani da za'a haifeshi face sai dai akan dabi'a ta sannin Allah, amma iyayen sa suna mai*

*dashi, bayahude ko banansame ko bama jushe."* (Buhari).

(b) Amma dalilin hankali shi ne wadannan halittu da suka gabata da wadanda za su zo nan gaba babu makawa akwai wanda ya halicce su, domin ba su iya samar da kansu, kuma bai kamata ace haka kawai aka samar da shi ba.

Kuma bai kamata ya samar da kan shi da kanshi ba, domin ba abinda yake halittar kansa, to kuma shi kafin a halicce shi ai babu shi to tayaya ya samar da halittar kan sa?.

Bai kamata ya samar da kansa ba, domin kowanne fararre babu makawa a akwai

wanda ya farar da shi, domin samuwar shi akan tsari na kaga shi, da kuma samuwar hadin garkuwar jiki tsakanin sababi da mai sabbaba shi da kuma tsakanin wasu abin da suka kasance tare da wasu masu hanawa kai tsaye, Samuwar hakan ba tare da wani da ya halicesu ba baya cikin tsari a wajan asalin samuwar sa, to ta yaya zai samar da tsarin rayuwa da wanzuwa?.

Idan kuma halitta ba za ta iya samar da kanta ba kuma shi ne Allah Ubangijin halittu baki daya.

Hakika Allah ya ambaci dalili na hankali da hujja kai tsaye a Suratu Tur, inda ya ce:

﴿ أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥ ﴾ الطور: ٣٥

**Ma'ana:** *"Halittar su ta zo ne hakanan koko sune ma masu halittar"*. Tur, aya ta:35.

Ma'ana halittar su ta kasance ne hakanan ba tare da an halicce su ba? Wannan sai ya nuna mana cewa Allah ta'ala shi ne wanda ya halicce su. Da haka ne lokacin da Jubairu da Muslim ya ji Manzon Allah yana karanta Suratu Tur, da ya kai ga wadannan ayoyin:

﴿ أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥ أَمۡ خَلَقُواْ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۚ بَل لَّا يُوقِنُونَ ٣٦ أَمۡ عِندَهُمۡ خَزَآئِنُ رَبِّكَ أَمۡ هُمُ ٱلۡمُصَيۡطِرُونَ ٣٧ ﴾ الطور: ٣٥ - ٣٧

**Ma'ana:** *"Shin an halicce su ne ba tare da wani abu ba, koko sune wadanda ma suka yi halittar. Koko sun halicci sammai da kasa ne, a'a ba dais a yi yakinine. Koko taskar Ubangijinka tana wurinsu ne? koko su ne masu karfi (akai)".* Suratu Tur, aya ta:35-37.

Shi kuma Jubairu da Mut'im a lokacin bai musulunta ba sai ya ce: *"Zuciya ta so ta tashi sama da hakane imani ya fara tabbata a zuciyata*. (Bukhari).

Za mu yi misali fayyatacce akan haka "Da, mutum zai yi shuka ya kewayeta sannan a zubo ruwa yana gudana, sai kuma ya ajiye kado da fito ya kuma kawanta sai ya ce ai wannan haka kawai ta kasance da kanta.

Mutane za su karyata shi, kuma za su maida shi wawa. Shin yanzu za'a iya cewa wadannan abubuwan su kasance da kansu har da sama da yadda take da tsarin ta ace ta samar da kanta haka kawai ta kasance ba tare da an samar da ita ba?.

a. Amma dalili na shari'ah shi ne littattafai da aka saukar daga sama gaba daya suna Magana akan haka da kuma abin da suka kunsa na gyara rayuwar halittu dalili daga Ubangiji masani mai hikima, domin gyaran al'ummah tare kuma da abunda ya zo na labarin abinda ya kasance, wacce mai zahirin abunda muke gani ya tabbatar da gaskiyar su shi ma dalili ne daga Allah

Ubangiji mai iko da ya zo da abinda ya bada labari.

b. Amma dalili na gababuwan jiki yana da fuska biyu. Na daya lalle mu muna ji kuma muna gani ta hanyar karba addu'a da kuma yaye damuwa, wacce ke nuni da cewa dalili ne kai-tsaye Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَنُوحًا إِذْ نَادَىٰ مِن قَبْلُ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ ﴾ الأنبياء: ٧٦

**Ma'ana:** *"Kuma Nuhu da ya kira (Ubangijin sa) tun kafin haka sai muka amsa masa"*. Suratul Anbiya'i, aya ta: 76.

Kuma ya ce:

﴿ إِذْ تَسْتَغِيثُونَ رَبَّكُمْ فَٱسْتَجَابَ لَكُمْ ﴾ الأنفال: ٩

**Ma'ana:** *"Ku tuna lokacin da kuka neman agajin Ubangijiku sai ya amsa muku".* Suratul Anfali, aya ta:9.

A cikin Hadisi kuma (Bukhari) ya ruwaito daga Anas dan Malik Allah ya kara masa yarda ya ce: *"Wani mutumin kauye ya zo ranar jumu'ah a lokacin Annabi (ﷺ) yana huduba sai yace ya kai Ma'aikin Allah! Dukiya ta hallaka, iyalai suna fama da yunwa, ka rokamana Allah(wato ana fama da karancin ruwa), sai Annabi (ﷺ) ya daga hannu sa ya yi addu'a sai ga girgije kwatan-kwacin tsauni, Annabi (ﷺ) bai sauka daga kan mimbari da face saida ya ga ruwa na zubowa daga gemun shi. A jumuah ta biyu*

*sai ga wannan mutumin kauyen ya tashi sai ya ce: Ya Ma'aikin Allah gini ya rushe dukiya ta nitse ka roka mana Allah! Sai Annabin Allah (ﷺ) ya daga hannunsa sai ya ce: "Ya Allah ka kawar da shi amma ba akan mu ba, bai gushe ba yana nuna wata nahiya ba har saida ya ruwan ya dauke"*.

Addu'ar mabukata bata gushe ba ta zama ana gani har a wannan lokacin na mu, ga wanda ya gashanta komawa ga Allah ta'ala kuma ya zo da sharuddan karbar addu'a.

Fuska ta biyu: Lalle ayoyin Annabawa wadanda ake kira mu'ujiza kuma mutane suka gansu ko suke ji ana karantawa hujja ce tsayyaya akan tabbatuwar manzanni, kuma

Allah ne ya aiko su domin lamari ne na daban da ya sabawa hangen mutum da Allah yake fitarwa domin karfafawa manzanni da ita da kuma taimakon su.

Misalin haka ayar da aka baiwa Annabi Musa (عَلَيْهِ السَّلَامُ) lokacin da aka umurce shi da ya doki kogi da sandar hannunsa sai ya doki kogin, nan taka sai kogin ya rabe kashi goma sha biyu hanyoyi suka bayyana busassu. Sai ruwan ya zamo kamar tsaunuka yadda suka yi kusurwa. Allah ya ce:

﴿ فَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱضْرِب بِّعَصَاكَ ٱلْبَحْرَ ۖ فَٱنفَلَقَ فَكَانَ كُلُّ فِرْقٍ كَٱلطَّوْدِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٦٣﴾ ﴾ الشعراء: ٦٣

**Ma'ana:** "Sai muka yi wahayi zuwa Masa da ka bugi kogi da sandar, sai ya rabe sannan kowanne kashi ya zama kamar tsauni mai girma". Suratush Shu'ara, aya ta: 63.

Misali na biyu: Ayar da aka baiwa Annabi Isah (عَلَيْهِ السَّلَامُ), yadda ya kasance yana raya matattu kuma yake fitar da su daga kabari da izinin Allah. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿وَأُحْيِ ٱلْمَوْتَىٰ بِإِذْنِ ٱللَّهِ﴾آل عمران: ٤٩

**Ma'ana:** *"Kuma nake rayar da matattu da izinin Allah"*. Suratu Ali Imran, aya ta:49.

﴿وَإِذْ تُخْرِجُ ٱلْمَوْتَىٰ بِإِذْنِي﴾المائدة: ١١٠

Kuma ya ce: **Ma'ana:** *"kuma kake fittar da matattu izinin na"*. Suratul Ma'idah, aya ta:110.

**Misali na Uku:-** Ayar da aka ba Annabi Muhammad (ﷺ) lokacin da Kuraishawa suka nemi a nuna musu aya (Mu'ujuza) sai ya yi nuni zuwa ga wata sai ya rabe kashi biyu mutane suka ganshi, a dalilin haka ne Allah yake cewa:

﴿ ٱقْتَرَبَتِ ٱلسَّاعَةُ وَٱنشَقَّ ٱلْقَمَرُ ۝١ وَإِن يَرَوْا۟ ءَايَةً يُعْرِضُوا۟ وَيَقُولُوا۟ سِحْرٌ مُّسْتَمِرٌّ ۝٢ ﴾ القمر: ١ - ٢

**Ma'ana:** *"Kiyama ta kusa wata ya rabe, kuma da suka ga ayar sai suka kauda kai suna cewa wannnan sihiri ne na gaba da*

*wanda muka sani"*. Suratul Kamar, aya ta:1-2.

Saboda wadannan ayoyin ne da Allah yake tafiyar da su ne yake karfafar manzannin sa ne, kuma don ya taimaka musu ne yake nuni ne kaitsaye akan kasantuwar Allah.

1. Imani da Ayyukan Allah. (Wato shi kadaine mahalicci ba shi da abokin tarayya kuma ba shi da mataimaki).

Ubangiji shi ne wanda mulki, halitta da tafiyar da lamari ke hannunsa, babu mai halitta sai Allah, babu mai cikakkiyar mallaka sai shi, lamari na gare shi. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ أَلَا لَهُ ٱلۡخَلۡقُ وَٱلۡأَمۡرُ ﴾الأعراف: ٥٤

**Ma'ana:** "Ku saurara halittu da lamura a gare shi suke". Suratul A'araf, aya ta:54. kuma ya ce:

﴿ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ لَهُ ٱلۡمُلۡكُۚ وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمۡلِكُونَ مِن قِطۡمِيرٍ ١٣ ﴾ فاطر: ١٣

**Ma'ana:** *"Wannan shi ne Ubangijinku mulki na gare shi, kuma wadannan da kuke kira kowa-bayansa ba sa mallakar komai na daga hancin dabino".* Fatir, aya ta:13..

A tarihi ba'asan wani da ya yi musun cewar Allah ba shi ne Ubangiji ba, saidai indai in ya kasance mai girman-kai ba mai yarda da

abinda ya kudirta ba, kamar yadda ya faru da Fir'auna a lokacin da ya ce wa mutanensa:

﴿أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلْأَعْلَىٰ ﴿٢٤﴾﴾ النازعات: ٢٤

**Ma'ana**: "Nine Ubangijin ku mafi daukaka". Suratun Nazi'at, aya ta:24.

Kuma ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَأُ مَا عَلِمْتُ لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرِى﴾ القصص: ٣٨

**Ma'ana:** "Ya ku ma'abota shawara ban san kuna da wani abin bauta ba bayan ni". Suratul Kasasi, aya ta: 38. Sai hakan bawai akan akida ba ce Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿وَجَحَدُواْ بِهَا وَٱسْتَيْقَنَتْهَآ أَنفُسُهُمْ ظُلْمًا وَعُلُوًّا﴾ النمل: ١٤

**Ma'ana**: *"Kuma sun musanta ta (ayoyin) kuma zukatansu sun tabbatar da gaskiyarta, kawai don zalinci da kuma girman-kai"*. Suratun Namli, aya ta:14.

Kuma Annabi Musa (عليه السلام) ya ce wa Fir'auna akan abin da ya fada mishi:

﴿لَقَدْ عَلِمْتَ مَآ أَنزَلَ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ بَصَآئِرَ وَإِنِّي لَأَظُنُّكَ يَٰفِرْعَوْنُ مَثْبُورًا ۝١٠٢﴾ الإسراء: ١٠٢

**Ma'ana:** *"Hakika ka sani ba wanda ya saukar saukar da wadannan face (Allah) Ubangijin sammai da kasa yana mai kulawa akai, kuma lalle ni ina zaton ka kai Fir'auna makaryacine"*. Suratul Isra'i, aya ta: 102.

Da haka ne mushirikai suka tabbata da rububiyar Allah, amma suka hada shi da wani a wajan bauta. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ قُل لِّمَنِ ٱلۡأَرۡضُ وَمَن فِيهَآ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ﴿٨٤﴾
سَيَقُولُونَ لِلَّهِۚ قُلۡ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿٨٥﴾ قُلۡ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلسَّبۡعِ
وَرَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡعَظِيمِ ﴿٨٦﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِۚ قُلۡ أَفَلَا تَتَّقُونَ
﴿٨٧﴾ قُلۡ مَنۢ بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَيۡءٖ وَهُوَ يُجِيرُ وَلَا يُجَارُ
عَلَيۡهِ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ﴿٨٨﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِۚ قُلۡ فَأَنَّىٰ تُسۡحَرُونَ
﴿٨٩﴾ ﴾ المؤمنون: ٨٤ - ٨٩

**Ma'ana:** *"Ka ce: Kasa da abin da ke cikin ta nawanene in kun kasance kuna sani? Da sannu za ce: Na Allah ne. Ka ce: To ba za ku yi tunani ba. Ka ce: Wanene Ubangijin*

*sammai bakwai kuma Ubangijin alarshi mai girma? Da sannu za su ce: Na Allah ne. Ka ce; To ba za ku ji tsoro ba. Ka ce; wanene birinkasar mulkin komai ke hannunsa yake bada kariya kuma ba ya neman kariya akan sa, in kun kasance kun sani? Da sannu za su ce; Na Allah ne. Ka ce; Ta yaya ake muku sihiri"*. Suratul Mu'uminun, aya ta: 84-89.

Kuma Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ خَلَقَهُنَّ ٱلْعَزِيزُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٩﴾ ﴾ الزخرف: ٩

**Ma'ana:** *"Kuma in ka tambaye su wa ya halicci sammai da kasai sai su ce; Allah ne*

*mahalicin su mabuwayi masani*". Suratuz Zukhruf, aya ta:9.

Kuma lamarin Ubangiji tsarkakken sarki gamamme ne ga lamarin kaddara da kuma shari'a, kamar yadda yake zartar da kasantuwar lamura haka kuma mai hukunta yadda yake so ne gwargwadon yadda hikimarsa ta hukunta, haka kuma yake shi ne mai hukunci akan kaddara da shari'arsa, da kuma hukuncin mu'amala ta yadda ya zartar da shi. To duk wanda ya riki wani tare da Allah mai shar'antawa a ibada ko mai hukunci a sha'anin rayuwa to hakika ya yi shirka kuma bai tabbatar da Imani ba.

**2. Imani da Kadaitakarsa.**

(Watau shi kadai ne abin bauta na gaske ba shi da abokin tarayya, kuma “ILAHU” ma’ana “ma’aluhu” watau abin ‘bauta’ ta hanyar so da girmamawa, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَإِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ ۖ لَّا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ الرَّحْمَٰنُ الرَّحِيمُ ﴿١٦٣﴾ ﴾ البقرة: ١٦٣

**Ma’ana:** *“Kuma abin bautawarku abin bautawane daya, babu abin bautawa sai shi, mai yawan rahma mai yawan jin kai”*. Bakara, aya ta: 163.

Kuma ya ce:

﴿ شَهِدَ اللَّهُ أَنَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَالْمَلَائِكَةُ وَأُولُو الْعِلْمِ قَائِمًا بِالْقِسْطِ ۚ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿١٨﴾ ﴾ آل عمران: ١٨

**Ma'ana:** *"Allah ya shaida lalle shi babu wani abin bauta sai shi haka ma mala'iku sun shaida da ma'abota ilimi babu wani abin bauta sai shi mabwayi mai hikima"*. Suratu Ali Imrana, aya ta: 18.

Kuma duk wanda ya riki wani abin bauta tare da Allah yana bauta masa, to tauhidinsan batacce ne, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ هُوَ ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ٦٢ ﴾ الحج: ٦٢

**Ma'ana:** *"Wannan, tare dacewa Ubangijinku Allah shi ne abin bauta na gaske kuma duk abin da kuke bautawa*

*bayan shi shine karya kuma lalle Allah shi ne madaukaki ne mai girma."* Hajji, aya ta: 62.

Kuma kiran wasu Alloli ba ya basu hakkin a bauta musu, Allah ya ce game da Lata a uzza da kuma manata:

﴿ إِنْ هِيَ إِلَّآ أَسْمَآءٌ سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ﴾ النجم: ٢٣

**Ma'ana:** *"Ai su ba komai ba ne saidai wadansu sunaye da kuka sanya musu ku da iyayanku da Allah bai saukar da wani daliliba akan su"*. Annajm, aya ta:23.

Kuma yace dangane da Annabi Yusuf (عليه السلام) lokacin da ya ce wa abokan zaman sa a kurkuku.

﴿ ءَأَرْبَابٌ مُّتَفَرِّقُونَ خَيْرٌ أَمِ ٱللَّهُ ٱلْوَٰحِدُ ٱلْقَهَّارُ ﴿٣٩﴾ مَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسْمَآءً سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ﴾يوسف: ٣٩ - ٤٠

**Ma’ana:** *“Shin abubuwan bauta ararrabe ne suka fi alheri ko Allah makadaici mai rinjaye, kuma ba abin da kuke bautawa bayan shi, sai dai wasu sunaye da kuka sanya musu ku da iyayanku Allah bai saukar da wata hujja akan su ba”.* Suratu Yusuf, aya ta: 39-40.

Da haka manzanin –tsira da amincin Allah ya tabbata a garesu- suka kasance suna fadawa mutanen su:

﴿ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ﴾ الأعراف: ٥٩

**Ma'ana:** *"Ku bautawa Allah ba ku da wani abin bauta bayan sa"*. A'araf, aya ta:59.

Sai dai mushrikai sun ki haka sai suka riki wani abin bauta koma bayan Allah, suna bauta masa tare da Allah mai girma kuma suna neman taimakon su suna kuma neman agajin su.

Hakika Allah ya bata wannan rikon allolin (wato abubuwan) da mushrikai suka yi ta bangarori biyu:

**Na daya:** Lalle wadnnan abubuwan bauta ba su da wani abu guda na abinda ya kebanci wanda za'a bauta wa. To ai ita ma halite ce, ba ta halitawa kuma ba ta anfanarwa ga

masu bauta mata, kuma ba ta kore mu su cuta kuma ba ta rike da rayuwarsu haka kuma mutuwa da rayuwa da kuma tayarwa. Allah ya ce:

﴿وَٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً لَّا يَخۡلُقُونَ شَيۡـًٔا وَهُمۡ يُخۡلَقُونَ وَلَا يَمۡلِكُونَ لِأَنفُسِهِمۡ ضَرًّا وَلَا نَفۡعًا وَلَا يَمۡلِكُونَ مَوۡتًا وَلَا حَيَوٰةً وَلَا نُشُورًا ٣﴾ الفرقان: ٣

**Ma'ana:** *"Kuma sun riki wani abin bauta bayansa (shi Allah) wadanda ba sa iya halittar komai kuma su ake halitta, kuma ba sa mallakawa kansu cutarwa ko amfanarwa haka ma ba sa mallakar mutuwa da rayuwa ta tayarwa"*. Suratul Furkan, aya ta;3. Kuma Allah ya ce:

﴿ قُلِ ٱدۡعُواْ ٱلَّذِينَ زَعَمۡتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِۖ لَا يَمۡلِكُونَ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا لَهُمۡ فِيهِمَا مِن شِرۡكٖ وَمَا لَهُۥ مِنۡهُم مِّن ظَهِيرٖ ٢٢ وَلَا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ عِندَهُۥٓ إِلَّا لِمَنۡ أَذِنَ لَهُۥ ﴾
سبأ: ٢٢ - ٢٣

**Ma'ana:** *"Ka ce; Ku kira wadanda kuke riyawa wadanda ba Allah ba, ba sa mallakar nauyin kwayar zarra a sammai haka kuma a kasa, kuma ba su da wani abu na tarayya kuma ba shi da wani mai taimako, kuma mai ceto ba ya amfanarwa a gabansa sai da izinin sa"*. Suratu Saba'i, aya ta:22-23.

Kuma Allah ya ce:

﴿ أَيُشۡرِكُونَ مَا لَا يَخۡلُقُ شَيۡـٔٗا وَهُمۡ يُخۡلَقُونَ ١٩١ وَلَا يَسۡتَطِيعُونَ لَهُمۡ نَصۡرٗا وَلَآ أَنفُسَهُمۡ يَنصُرُونَ ١٩٢ ﴾ الأعراف: ١٩١ - ١٩٢

**Ma'ana:** *"Yanzu sais u yi tarayya da wadanda ba sa halittar komai kuma su ake halitta, kuma ba sa iya taimakonsu kuma ba sa iya taimakon kawunan su".* A'ara, ya ta: 191-192.

Idan wannan halin ya kasance haka na bautawa wanin Allah, to riko da shi ya kasance wauta ne kuma mafi bacewa.

**Na biyu:-** Lalle wadannan mushrikan sun kasance suna tabbatar da ce wa Allah daya ne Ubangiji mahalcici wanda mallakar komai ke hannunsa, kuma shi ke rinjaye ba'a rinjayarsa, ta wannan ya zama dole a bauta masa ta hanyar kadaita shi kamar yadda

suka kadaita shi da ayyukan sa, Allah madaukaki ya ce:

﴿ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٢١﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ فِرَٰشًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ فَلَا تَجْعَلُوا۟ لِلَّهِ أَندَادًا وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٢٢﴾ ﴾ البقرة: ٢١ - ٢٢

**Ma'ana:** *"Ya ku mutane ku bauta wa Ubangijin ku wanda ya halicce ku da wadanda suka kasance kafin ku tsammaninku za ku samu takwa. Shi ne wanda ya shinfida muku kasa kuma ya gina muku sama sannan ya saukar muku da ruwa daga sama sai ya fitar da shi da 'ya'yn itatuwa don ya zama arziki a gareku,*

*saboda haka kar ku sanya wa Allah kishiya alhalin kuma sane”*. Bakara, 21-22.

Kuma ya ce:

﴿ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَهُمْ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۖ فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿٨٧﴾ ﴾
الزخرف: ٨٧

**Ma’ana:** *“Idan ka tambaye su wa ya halice su sai suce maka Allah ne saboda haka mune zaku koma gare su”*. Suratuz Zukhruf, aya ta: 87.

Kuma ya ce:

﴿ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ أَمَّن يَمْلِكُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ
وَمَن يُخْرِجُ ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَىِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ ۚ

فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُ ۚ فَقُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٣١﴾ فَذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمُ ٱلْحَقُّ ۖ فَمَاذَا بَعْدَ ٱلْحَقِّ إِلَّا ٱلضَّلَٰلُ ۖ فَأَنَّىٰ تُصْرَفُونَ ﴿٣٢﴾ يونس: ٣١ - ٣٢

**Ma'ana:** *"Ka ce wa ke azurta ku daga sama da kasa ko wake mallake da sama da kasa ko wake mallake da jin ku da ganinku kuma wake fitar da rayayye daga matacce kuma wa ke fitar da matacce daga rayayye kuma wa ke juya lamura?. Da sannu za su ce Allah ne, ka ce mu su ba za ku ji tsoron Allah ba?. To wannan shi ne Ubangijinku na gaske, to menene bayan gaskiya ai sai bata, to ta yaya ake juyar da ku."*? Suratu Yunus, aya ta:31-32.

- **Imani da sunayensa da kuma siffofinsa.**

(watau tabbatarwa Allah abinda ya tabbatar wa kansa a littafin sa ko cikin sunnar manzonsa, na sunaye da suffofi akan yadda suka dace da shi, ba tare da canzawa ba ko tawali ko misiltawa ko kamantawa ba. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ وَذَرُواْ ٱلَّذِينَ يُلۡحِدُونَ فِيٓ أَسۡمَٰٓئِهِۦۚ سَيُجۡزَوۡنَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٨٠﴾ الأعراف: ١٨٠

**Ma'ana:** *"Kuma Allah na da sunaye masu mafiya kyawu saboda haka ku kira shi da su, kuma ku kaurace wa wadannan da suke canza sunayen sa da sannu za'a sakanka musu da abin da suka kasance suna*

*aikatawa"*. Suratul A'araf, aya ta:180. Kuma ya ce:

﴿وَلَهُ ٱلۡمَثَلُ ٱلۡأَعۡلَىٰ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢٧﴾
الروم: ٢٧

**Ma'ana:** *"Kuma shi ke da siffa madukaka a sama da kasa, kuma shi ne mabuwayi mai hikima"?*. Suratr Rum, aya ta: 27. Kuma ya ce:

﴿لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ١١﴾
الشورى: ١١

**Ma'ana:** *"Ba shi da wani wanda ya yi kama da shi, kuma shi mai ji ne mai gani".* Suratus Shurah, aya ta: 11.

Kuma lalle bangarori biyu sun bata game da wanna lamari.

**Ta farko:-** Masu sharewa, sune wadanda suka musanta sunayen Allah da siffofinsa ko wani sashi na hakan, suna riya cewa tabbatar wa Allah da siffofi yana lizimata kamantawa, wato a siffanta Allah da halitunsa, wannan abin da suke riyawa batane ta hanyoyi masu zuwa:

**Hanya Ta daya:-** Sun ce lalle hakan yana lizimta wadansu abubuwa da ba su dakyau, kamar tufka-da-war-wara ga kalaman Allah tsarkaken sarki, saboda Allah ta'ala ya tabbatar wa kansa sunaye da siffofi, kuma ya kore wa kansa kamanceceniya da wani abu, ko da ko tabbatarwar ta lizimta kamanceceniya, to ko hakan yana zama

tufka-da-war-wara a maganar Allah da kuma ace sashi yana karyata sashi.

**Hanya Ta biyu:-** Lalle shi ba ya lizimta cewa don abubuwa biyu sun hadu a suna ko siffa ta kasance abin kamantawa, to kuma ka ga mutane biyu suna dai-dai a wajan ji da gani da magana amma ba ya zama dole su kasance wajan magana da ji da sauraro ba ya zama daya, kuma zaka ga dabba tana da hannu da kafa da ido kuma haka ba ya zama cewa gabubuwan suna kama. Idan hakan ya bayyana a tsakanin halittu akan abin da suka yi ittifaki ko siffa to wannan shima haka yake tsakanin halitta da mahalicin su wanda yake bayyana mai girma.

**Bangaren Na Biyu:**- Masu kamantawa, wadanda suka tabbatar wa Allah sunaye da sfifofi tare da kamanta Allah da halitunsa suna riya cewa yana dai-dai da dalili na nassi domin Allah ya yi magana da bayin sa game da abin suke fahimta, wannan abin da suka riya karya ne ta fuskoki masu zuwa:

**Na daya:**- Lalle kamanta Allah da halitunsa lamari ne batacce, kuma shari'a da hankali sun kore hakan, sannan kuma ba ya kamata ace ainda nassoshin littafin Allah da hadisin Manzonsa suke nunawa ace akwai lamarin wargi a ciki.

**Na biyu:-** Allah yana Magana da bayin sa har yada zasu fahimci ma'anar, amma sanin

hakikanin ma'anarsa da hakikanin yadda yak Allah kadai ya barwa kansa sani na abinda ya shai zatinsa da kuma siffofinsa.

To idan Allah ya tabbatar wa da kansa ji, cewa lalle shi yana ji, to lalle ji sananne ne ta asalin ma’ana. (wato shi ne fahimtar murya), saidai hakikanin wannan na Allah madaukakin sarki to ba wanda ya sani, domin hakikakanin ji ma ya banbanta a tsakanin halitta, to idan haka ne banbani ma tsakanin na Allah da na halittu shi ya nisa ya kuma fi girma.

Idan Allah ya bada labari game da kansa cewa shi ya dai-daita akan alarshi to lalle ***istiwa’i*** daidaituwa ta bangaren ma'ana

sananniyace, amma saidai hakikanin *istiwa'i* (daidaituwar) da shi Allah madaukakin sarki yake akanta ba wanda ya sani, ta yadda za'ace ga yadda Allah ya daidaita akan al'arshinsa. Domin ita daidaituwar ma a ta banbanta a tsakanin halittarsa, ai daidaituwa akan kujera tabbataciya ba kamar daidaituwa bane akan sirdin rakumi mai wahala. Idan haka ya banbanta a tsakanin halitta to ya banbanta a tsakanin halitta da Mahalici shi ya fi kuma shi yafi girma.

Kuma imani da Allah akan abinda muka siffanta Allah da shi yana gadar wa da

mumini amfani masu girma daga cikin akwai:-

**Na daya:-** Tabbatarwa Allah kadaitaka ta yadda babu wani abin kauna sai shi, kuma babu wanda za’a ji tsoro sai shi haka kuma babu wanda za’a bautawa sai shi.

**Na biyu:-** Cikakkiyar soyoyya ga Allah ta’ala da girmama shi da abin da sunayansa da siffofin sa madaukaka suka hukunta.

**Na Uku:-** Tabbatar da bauta masa, ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi da kuma nisanta daga abinda ya yi hani da shi.

- **IMANI DA MALIKU.**

**Maliku:** (Wata halitta ce ta boye wadanda aka halicce domin su bautawa Allah, ba su da wani kaso na rububiya ko uhiyya ko kadan, Allah ya halicce su ne daga haske kuma ya yi musu baiwa akan cikakkiyar yarda da umurnin sa gaba daya, da kuma karfin zartar da al'amarinsa). Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَمَنْ عِندَهُۥ لَا يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَلَا يَسْتَحْسِرُونَ ١٩ يُسَبِّحُونَ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ لَا يَفْتُرُونَ ٢٠ ﴾ الأنبياء: ١٩ - ٢٠

**Ma'ana:** *"Kuma wadanda suke tare da shi ba sa girman kai daga barin bautar sa kuma ba sa gajiya. Suna tasbihi dare da yini basu gajiya"*. Anbiya'i, aya tta:19-20.

Kuma suna da adadi masu yawa babu wanda ya san adadin sai Allah. Hakika ya tabbata a cikin hadisi daga Anas ﷺ Allah ya yarda da shi a labarin mi'iraji lalle Annabi ﷺ an daga shi zuwa baitul ma'mur a can sama wanda malaiku dubu saba'in ne ke sallah a cikin sa idan suka fita ba sa dawowa sai dai wasun su.

**Imani da malaiku yana kunshe da lamura hudu ne:-**

1. Imani da kasancewar su.

2. Imani da wadanda muka san sunayensu kamar Jibril ﷺ da wadanda ma bamu sani ba, za mu yi imani da su a dunkule.

3. Imani da abin da aka siffanta su da shi, kamar yadda Annabi ﷺ ya ba mu labari cewa ya ga Jibril a ainihin halitarsa wacce aka halicce shi yana da fukafukai dari shida kuma ya tokare ko'ina.

Hakika mala'iku suna rikida da umurnin Allah zuwa siffar mutane, kamar yadda ya faru da Jibril ﷺ a lokacin da aka aike shi zuwa na Nana Maryam ya zo mata a siffar mutane, da kuma lokacin da ya zo wurin manzon Allah ﷺ ya zauna a cikin sahabban

sa ya yi tambaya game da addinin musulunci tare da martabobinsa. (Imamu muslim).

Haka kuma mala'ikun da Allah ya aika zuwa ga Annabi Ibrahim ﷺ inda suka kasance a sifffar mutane.

1. Imani da abin da aka sanar da mu na ayyukansu wandanda suke aikatawa da umurnin Allah, kamar tasbihi da bauta masa dare da yi ba tare da gajiya ko kasawa ba.

**Hakika wasu kuma suna da wani aiki da aka tsara masu.** Misali:-

**Jibril** ﷺ amitacce ya dauko wahyin Allah zuwa ga annabawa da manzanni.

**Mikail** ﷺ wanda ke kula da ruwan sama da tsiro.

**Israfil** ﷺ wanda ke busa kaho a lakocin kiyama da tayar da mutane.

**Malakul Maut** ﷺ:- wanda ke daukar rayuwa.

**Malik** ﷺ wanda ke gadin wuta.

**Mala'iku**:- Masu kula da rayuka a cikin mahaifa, idan ya kai wata hudu sai Allah ya aika mala'ika ya busa rai ya rubuta arzikin sa da aikinsa da kuma makomarsa.

**Maliku** masu kula da ayyukan bani Adam kuma suke rubuta wa kowanne mutum, dayansu na dama daya kuma na hagu.

**Malaiku** masu tambaya a kabari, idan aka sa mutum a cikin kabari malaiku biyu za su zo suna tamyarsa game da Addinin sa, Annabinsa, da kuma Ubangijinmu.

**- Imani da mala'iku yana gadarwa mumini amfani kamar haka:**

1. Ilimi da sanin girman Allah da karfin sa da da karfin sarautarsa domin kasancewar girmar halitta na nuna girman mahalicci.

2. Godiya ga Allah akan kulawar sa ga bani Adam, ta yadda ya sanya malaiku suna tsare da su kuma suna rubuta ayyukan su da wanin haka na kyautatawa.

3. Soyayya ga malaiku ta yadda suka tsayu da umurnin Allah.

Hakika wasu mutane karkatattu sun karyata kasantuwar mala'iku suna da jiki, suka ce wadansu ibara ce masu karfi daga cikin halitta. Irin wannan karyatawar ne ga littafin Allah da Hadisin Manzonsa ﷺ da kuma ijama'in musulmi.

Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ جَاعِلِ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُوْلِيٓ أَجۡنِحَةٖ مَّثۡنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَ ﴾ فاطر: ١

**Ma'ana:** “Dukka godiya ta tabbata ga Allah makirkirin sammai da kassai wanda ya mala'iku manzanni ma’abota fukafukai biyu-biyu, uku-uku, da hudu-hudu”.Suratu Fatir, aya ta:1.

Kuma ya ce:-

﴿ وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذۡ يَتَوَفَّى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يَضۡرِبُونَ وُجُوهَهُمۡ وَأَدۡبَٰرَهُمۡ ﴾ الأنفال: ٥٠

**Ma'ana:** “Da zaka ga lokacin da mala'iku suke karbar rayukan kafirai suna bugun fuskokin su da bayan su”. Suratul Anfal, aya ta:50.

Kama ya ce:-

﴿ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِى غَمَرَٰتِ ٱلْمَوْتِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓا۟ أَيْدِيهِمْ أَخْرِجُوٓا۟ أَنفُسَكُمُ ﴾الأنعام: ٩٣

**Ma'ana**: *"Da zaka ga lokacin da azzalumai ke magagin mutuwa lokacin da mala'iku suka baza hannuwansu suna cewa ku fito da rayukan ku"*. Suratul An'am, aya ta:93.

Kuma ya ce:

﴿ حَتَّىٰٓ إِذَا فُزِّعَ عَن قُلُوبِهِمْ قَالُوا۟ مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ ۖ قَالُوا۟ ٱلْحَقَّ ۖ وَهُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْكَبِيرُ ﴿٢٣﴾ ﴾ سبأ: ٢٣

**Ma'ana:** *"Har zuwa lokain da aka ire tsoro daga zukatansu sai su ce me Ubangijinku ya ce sai su*

*ce ya fadi gaskiya, kuma shi ne madaukaki mai girma"*. Suratu Saba'i, aya ta:23.

Kuma ya ce ga 'yan aljanna:

﴿وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَدْخُلُونَ عَلَيْهِم مِّن كُلِّ بَابٍ ﴿٢٣﴾ سَلَٰمٌ عَلَيْكُم بِمَا صَبَرْتُمْ ۚ فَنِعْمَ عُقْبَى ٱلدَّارِ ﴿٢٤﴾﴾ الرعد: ٢٣ - ٢٤

**Ma'ana:** *"Mala'iku suna shiga a gare su ta kowacce kofa (suna cewa); Aminci ya tabbata a gareku' game da kuka yi na hakuri, madalla da gidan karshe"*. Suratur Ra'ad, aya ta: 23-24.

A cikin Sahihil Bukhari daga Abi Hurairah ﵁ daga Annabi ﷺ ya ce: *"Idan Allah ya so bawa sai ya kira (mala'ika) Jibrilu (ya ce) Allah yana son wane ka so shi, sai (mala'ika)*

*Jibrilu ya so shi, sai (mala'ika) Jibrilu ya yi shile ga halittun sama Allah yana son wane to ku so shi, sai duk su so shi, sannan ya sanya masa yarda a bayan kasa*".

A cikin sa (Bukhari) kuma dai Annabi ﷺ ya ce: *"Idan Jumu'ah ta kasance mala'iku suna tsayuwa a kofar masallaci suna rubuta sunayan wadanda suka zo masallaci daya-bayan-daya har sai liman ya hau mimbari sai su rufe littafin, su koma suna sauraron huduba*".

Wannan nasoshi da suka tabbata a fili yake cewa malai'ku jikine ba kawai karfi ba ne na ma'ani ba kamar yadda karkatattu suka

fada. Kuma akan wadannan nassoshi ne musulmai suka yi ijma'i.

# - IMANI DA LITTATTAFAI.

"Kutub" Jama'i ne na "Kitabun" ma'ana abin da aka rubuta. Abin nufi anan shi ne (Littafin da Allah ya saukar ga Annabawan sa don zama rahama gahalitta domin shiryar da su don su samu rabo duniya da lahira).

**Imani da littafi yana kunsar abubuwa hudu, kamar haka:-**

1. Imani da cewa Allah ne ya saukar da su.

2. Imani da sunayen su da aka saukar, misali AlKur'ani ga Annabi Muhammad ﷺ da (AttauraH) ga Annabi Musa عليه السلام da (Injila) ga Annabi Isa عليه السلام da kuma (Zabura) ga Annabi Dawud عليه السلام , da ma wadanda ba mu sani ba.

1. Gasgantawa ga dukkan labarin da ya inganta na su, kamar labaran da ke cikin Alkur'an da kuma lambaran da ba'a canza ba na littattafan da suka gabata.

2. Aiki da hukuncin da ba'a share ba, yarda da mika wuya da shi, daya ne mun fahimci hikimar ko ba mu fahimta ba. Dukkan littattafan da suka sauka to Alkur'ani ya share su, Allah ta'ala ya ce:

﴿وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَمُهَيْمِنًا عَلَيْهِ﴾ المائدة: ٤٨

**Ma'ana:** "Kuma mun saukar da littafi zuwa gare ka da gaskiya wanda ke gaskanta abin da ke gaba gareshi na

littafi kuma yana sharewa game dasu". (wato mai kafa hujja a kansu). Suratul Ma'idah, aya ta 48.

Da haka ba ya halasta ayi hukunci da duk wani abu daga cikin littattafan da suka gabata. Sai dai abin da ya inganta kuma Kur'ani ya tabbatar da shi.

**Imani da littafi yana gadarwa mamini da amfani kamar haka:**

1. Sanin cewa Allah ya sanya kulawa ga bayinsa ta yadda ya ba kowacce al'umma littafi domin shiriyar da su.

2. Sanin hikimar Allah madaukakin sarki a shari'arsa ta yadda ya shar'anta wa alumma abin da ya dace da ita, na rayuwa kamar yadda ya ce:

﴿لِكُلٍّ جَعَلْنَا مِنكُمْ شِرْعَةً وَمِنْهَاجًا﴾ المائدة: ٤٨

**Ma'ana:** *"Ko wace al'umma mun saya mata shari'ah da tsari"*. Suratul Ma'idah, aya taa:48.

1. Godiya akan ni'imomin Allah a kan haka.

**IMANI DA MANZANNI.**

**Rusul**:- Jama'i ne na 'Rasul' watau wanda aka aiko, mai isar da sako.

Abin nufi a nan (wanda aka yi masa wahayi daga cikin mutane da Shariah kuma aka yi masa umarni da isarwa) na farkon su shi ne Annabi Nuhu ﷵ na karshen su kuma shi ne Annabi Muhammad ﷺ.

Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ إِنَّآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ كَمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ نُوحٖ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ ﴾
النساء: ١٦٣

**Ma'ana:** *"Hakika mu mun yi wahayi (da littafi) zuwa gareka kamar yadda muka yi wahayi ga Nuhu da Annabawan da suka zo bayan sa"*. Surratun Nisa'i, aya ta:173.

A cikin hadisin Bukhari daga Anas dan Malik (A cikin hadisin ceto) Lalle Annabi ﷺ ya ce: *"An ambaci cewa mutane za su je wurin (Annabi) Adam don ya cece su sai ya basu uzuri, sai ya ce: Ku tafi zuwa ga (Annabi) Nuhu farkon Manzo wanda Allah ya aiko*". Har karshen Hadisin.

Kuma Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ﴾الأحزاب: ٤٠

**Ma'ana:***"Annabi Muhammad bai kasance uba na daya daga cikin manzan ku ba, sai dai Manzon Allah ne kuma cikamakin Annabawa"*. Suratul Ahab, aya ta:40.

Kuma mutane ba su taba fadawa cikin bata ba face sai da aka aiko musu da Manzo ya karantar da su shariah. Ko Annabi wanda aka yi wa wahayi don ya tabbatar da ita, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَ ﴾النحل: ٣٦

**Ma'ana:** *"Kuma hakika mun aika wa kowacce alummah da manzo (suna cewa)*

*Ku bautawa Allah kuma ko nisanci dagutu"*.

Suratn Nahli, 36.

Kuma ya ce:

﴿ وَإِن مِّنْ أُمَّةٍ إِلَّا خَلَا فِيهَا نَذِيرٌ ﴿٢٤﴾ ﴾ فاطر: ٢٤

**Ma'ana:** *"Babu wata alummah face mun aika da mai gargadi"*. Fatir, aya ta:24.

Kuma Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ إِنَّآ أَنزَلْنَا ٱلتَّوْرَىٰةَ فِيهَا هُدًى وَنُورٌ ۚ يَحْكُمُ بِهَا ٱلنَّبِيُّونَ ٱلَّذِينَ أَسْلَمُوا۟ لِلَّذِينَ هَادُوا۟ ﴾ المائدة: ٤٤

**Ma'ana:** *"Lalle mu mun saukar da Attaurah a cikinta akwai shiriya da haske, Annabawan da suka sallama suna hukunci da ita ga Yahudawan"*. Ma'adah, aya tta:44.

Kuma manzanni (mutane ne wadanda aka haliccce ba su da wata siffa ta rububiyya ko uluhiyya, wato ba su halitta ba kuma ba su cancanci a bauta musu ba).

Allah madaukakin sarki ya ce game da Annabinsa Muhammad ﷺ kuma shi ne shugaban manzanni, mafi girma matsayi a wurin Allah:

﴿ قُل لَّآ أَمۡلِكُ لِنَفۡسِي نَفۡعٗا وَلَا ضَرًّا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۚ وَلَوۡ كُنتُ أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ لَٱسۡتَكۡثَرۡتُ مِنَ ٱلۡخَيۡرِ وَمَا مَسَّنِيَ ٱلسُّوٓءُۚ إِنۡ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٞ وَبَشِيرٞ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ١٨٨ ﴾ الأعراف: ١٨٨.

**Ma'ana:** *“Kace lalle ni ba na iya mallakar wa kaina amfanarwa ko (karewa kai na) cuta sai abin da Allah ya so, da na kasance*

*masanin gaibi da na yawaita alheri kuma da sharri bai same ni ba, sai dai ni mai gargadi ne kuma mai bushara ne ga mutanen da suke yin imani”*. Suratul A'araf, aya ta:188.

Allah ya ce:

﴿ قُلْ إِنِّي لَآ أَمْلِكُ لَكُمْ ضَرًّا وَلَا رَشَدًا ﴿٢١﴾ قُلْ إِنِّي لَن يُجِيرَنِي مِنَ ٱللَّهِ أَحَدٌ وَلَنْ أَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلْتَحَدًا ﴿٢٢﴾ ﴾ الجن: ٢١ - ٢٢

**Ma'ana:** *“Ka ce lalle bana mallaka mu ku (tunkude) cuta ko amfanarwa ba, ka ce: Lalle ni babu wani da zai kare ni kuma ban samu wanda yake koma bayan shi wanda zan kadaita ba”*. Suratul Jinn, aya ta:21-22.

Kum abubuwan da ke samun mutane na rashin tafiya yana samun su (Manzannin)

haka na mutuwa da bukatar abinci da abin sha da wanin haka, Allah ya ce game da (Annabi) Ibrahim ﷺ akan yadda ya siffanta shi:

﴿ وَٱلَّذِى هُوَ يُطْعِمُنِى وَيَسْقِينِ ﴿٧٩﴾ وَإِذَا مَرِضْتُ فَهُوَ يَشْفِينِ ﴿٨٠﴾ وَٱلَّذِى يُمِيتُنِى ثُمَّ يُحْيِينِ ﴿٨١﴾ ﴾ الشعراء: ٧٩ - ٨١

**Ma'ana:** *"Kuma shi ne wanda ke ciyar dani kuma yake shayar da ni, idan na yi rashin lafiya shi ke bani lafiya, kuma shi ne wannan da yake kashe ni kuma ya rawani"*.! Suratus Shu'ara'i, aya ta:79-81.

Kuma Annabi ya ce: "Lalle ni mutune irin ku ina mantuwa kamar yadda kuke mantuwa, idan na manta ku tuna mani".

Hakika Allah ya siffanta su da mafiya bauta dudda girman matsayin su, a cikin siyakin yabo a kan su sai ya ce dangane da Annabi Nuhu ﷵ :

﴿ إِنَّهُۥ كَانَ عَبۡدٗا شَكُورٗا ۝٣ ﴾ الإسراء: ٣

**Ma'ana**: *“Lalle shi ya kasance bawa ne mai godiya”*. Suratul Isra'i aya ta: 3.

kuma ya ce dangane da Annabi Muhammad ﷺ:

﴿ تَبَارَكَ ٱلَّذِي نَزَّلَ ٱلۡفُرۡقَانَ عَلَىٰ عَبۡدِهِۦ لِيَكُونَ لِلۡعَٰلَمِينَ نَذِيرًا ۝١ ﴾ الفرقان: ١

**Ma'ana:** *“Albarka ta cika ga wanna da ya saukar ga bawan sa Alfurkan domin ya*

*kasance mai gargadi ga mutane"*. Suratul Fulkana, aya ta:1.

Haka kuma ya ce dangane da Annabbi Ibrahim da Annabi Is'hak da kuma Annabbi Yakub, amincin Allah ya tabbata a garesu:

﴿ وَٱذۡكُرۡ عِبَٰدَنَآ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ أُوْلِي ٱلۡأَيۡدِي وَٱلۡأَبۡصَٰرِ ٤٥ إِنَّآ أَخۡلَصۡنَٰهُم بِخَالِصَةٖ ذِكۡرَى ٱلدَّارِ ٤٦ وَإِنَّهُمۡ عِندَنَا لَمِنَ ٱلۡمُصۡطَفَيۡنَ ٱلۡأَخۡيَارِ ٤٧ ﴾ ص: ٤٥ - ٤٧

**Ma'ana:** *"Ka ambaci bayin mu Ibrahim da Is'hak da Yakub ma'bota karfi da gani. Lalle mu mun tsarkake su da tsarkaka na gida mai Ambato. Kuma lalle su a wurin mu tabbas suna daga cikin zababbu wadanda aka zaba"*. Suratu Sad, aya ta:45-47.

Kuma ya ce game da Annabi Isah ﷺ da Nana Maryam:

﴿إِنْ هُوَ إِلَّا عَبْدٌ أَنْعَمْنَا عَلَيْهِ وَجَعَلْنَٰهُ مَثَلًا لِّبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٥٩﴾ الزخرف: ٥٩

**Ma'ana:** *"Shi dai kawai bawa ne wanda muka yi wa ni'ima kuma muka sanya shi ya zama misali ga bani Israil"*. Suratu Zukhruf, aya ta:59.

Kuma Imani da manzanni ya kunshi lamura hudu ne:-

1. Imani da cewa sakon su gaskiya ne daga wurin Allah, duk wanda ya kafirce wa sakon daya daga cikin su to hakika ya kafarce musu

gaba dayansu, kamar yadda Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿كَذَّبَتْ قَوْمُ نُوحٍ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٠٥﴾﴾ الشعراء: ١٠٥

**Ma'ana:** *“Hakika mutanen Nuhu sun karyata manzanni”*. Shu'ara'i, aya ta:105.

Sai Allah ya sanya su masu karyata dukkan manzanni tare da cewa babu wani manzo bayan shi da suka karyata, haka kuma nasara da suka kuryata Annabi Muhammad ﷺ ba su bi shi ba sai suka zama masu karyata Annabi Isah dan Nana Maryam ؈ ba tare da sun bi shi ba, musamma lokacin da ya yi bushara da zuwan Annabi Muhammad ﷺ, kuma ya nuna musu cewa

zai zo ne ya tseratar da su daga bata kuma ya shiryar da su zuwa ga hanya madaidaiciya.

1. Imani da sunan wadanda aka sanar da mu sunayansu: Misali Annabi Muhammadﷺ, da Annabbi Ibrahim عليه السلام, Annabi Musa عليه السلام, Annabi Isah عليه السلام, Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a garesu baki-daya) wadannan biyar din sune; Ulul azmi daga cikin manzannin Allah madaukakin sarki ya ambace su a AlKur'ani a wurare biyu; Suratul Ahzab sai ya ce:

﴿ وَإِذْ أَخَذْنَا مِنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِيثَٰقَهُمْ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٍ وَإِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ ﴾ الأحزاب: ٧

**Ma'ana:** *"Tuna lokacin da muka rika daga Annabawa alkawarin su da kuma kai (Annabi) da Nuhu da Ibrahim da Musa da Isah dan Maryam"*. Aya ta:7. Haka ma cikin Suratul Shura ya ce:

﴿ ۞ شَرَعَ لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ وَمَا وَصَّيۡنَا بِهِۦٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓۖ أَنۡ أَقِيمُواْ ٱلدِّينَ وَلَا تَتَفَرَّقُواْ فِيهِۚ ﴾الشورى: ١٣

**Ma'ana:** *"An shar'anta muku addinin da aka yi wa Nuhu wasici da shi da kuma wadanda muki yi wahayi gare ka, haka kuma da duk abunda muka yi wasici da shi ga Ibrahim da Musa da Isah cewa su tsayar da addini kar su raraba a cikin sa"*. Aya ta: 13.

Amma duk wanda bamu san sunanshi daga cikin sub a munyi imani dashi a dunkule. Allah yace: “Hakika mun aiko manzanni kafin kai daga cikin akwai wadanda muka baka labari kuma daga ciki akwai wadanda bamu baka labarin su ba”.

2. Gaskanta dukkan abin da ya inganta daga garesu wanda suka bada labari.

Amma wanda ba mu san sunansa ba daga cikinsu sai mu yi Imani da shi a dunkule, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ وَرُسُلًا قَدْ قَصَصْنَٰهُمْ عَلَيْكَ مِن قَبْلُ وَرُسُلًا لَّمْ نَقْصُصْهُمْ عَلَيْكَ ﴾النساء: ١٦٤

**Ma'ana:** *Kuma da manzanni da hakika mun baka labarinsu tuntuni, da kuma manzanni da ba mu baka labarrinsu ba"*. Suratun Nisa'i, aya ta:164.

3. Aiki da shri'ar wanda aka aiko mana da shi a matsayin Manzon, kuma shi ne cikon su wato Annabbi Muhammad (Tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi), wanda aka aiko ga dukkan mutane. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ فَلَا وَرَبِّكَ لَا يُؤۡمِنُونَ حَتَّىٰ يُحَكِّمُوكَ فِيمَا شَجَرَ بَيۡنَهُمۡ ثُمَّ لَا يَجِدُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَرَجٗا مِّمَّا قَضَيۡتَ وَيُسَلِّمُواْ تَسۡلِيمٗا ٦٥ ﴾ النساء: ٦٥

**M'ana:** *"Wallahi ba za su yi imani ba har sai sun sanya ka mai hukunci a abinda ke gudana tsakanin su, sanan ba su sami wata damuwa a zuciyan su ba akan abinda ka hukunta kuma su sallama hakikanin sallamawa"*. Suratun Nisa'i, aya ta:65.

Imani da manzani akai amfanuwar shi ga mumini kamar haka:

**Na farko:-** Sanin rahmar Allah da kulawar sa ga bayin sa, yadda ya aike musu da manzanni don su nuna musu tafarkin Allah ta'ala, kuma su bayyana musu yadda za su bauta mishi, domin hankalin mutum kadai ba zai iya tabbatarmai da hakan ba.

**Na biyu:-** Godiya ga Allah ta'ala akan wanna ni'ima mai girma.

**Na uku;-** Son manzannin da girmama su da kuma yaba musu akan abin da ya cancance su, domin su manzannin Allah ne, kuma sun tsayu matuka wajan bauta da isar da sako da kyakyawar mu'amala ga bayinsa.

Kafirai sun karyata manzanin su suka ce manzannin Allah ba mutane ba ne. Hakika Allah ya ambaci wannan zancen, ya kuma karyata su da fadin cewa:

﴿ وَمَا مَنَعَ ٱلنَّاسَ أَن يُؤْمِنُوٓا۟ إِذْ جَآءَهُمُ ٱلْهُدَىٰٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓا۟ أَبَعَثَ ٱللَّهُ
بَشَرًا رَّسُولًا ﴿٩٤﴾ قُل لَّوْ كَانَ فِى ٱلْأَرْضِ مَلَٰٓئِكَةٌ يَمْشُونَ

مُطْمَئِنِّينَ لَنَزَّلْنَا عَلَيْهِم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ مَلَكًا رَّسُولًا ﴿٩٥﴾
الإسراء: ٩٤ - ٩٥

**Ma'ana:** *"Babu abin da ya hana mutane yi imani bayan shiriya ta zo masu sai don sun ce; Ya Allah zai aiko da mutum a matsayin manzo?. Ka ce da mala'iku ne a bayan kasa su ke tafiya cikin natsuwa da mun saukar musu da mala'ika a matsayin manzo"*. Suratul Isra'i, aya ta:95-94.

Allah ya karyata su ya kuma nuna cewa babu makawa saidai mutum ne zai kasance a matsayin Manzo a bayan kasa matukar mutane ne, amma da kuwa mala'iku ne to da mun saukar da mala'ika a matsayin manzo. Domin ya kasance irin su. Da haka

ne Allah ya hikayo wa wadanda suka karyata manzanni lokacin da suka ce:

﴿إِنْ أَنتُمْ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا تُرِيدُونَ أَن تَصُدُّونَا عَمَّا كَانَ يَعْبُدُ
ءَابَآؤُنَا فَأْتُونَا بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ١٠ قَالَتْ لَهُمْ رُسُلُهُمْ إِن نَّحْنُ إِلَّا
بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَمُنُّ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَمَا كَانَ
لَنَآ أَن نَّأْتِيَكُم بِسُلْطَٰنٍ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ﴾ إبراهيم: ١٠ - ١١

**Ma'ana:** *“Ku mutane ne irin mu kuma kuna son ku hana mu bauta wa abin da iyayen mu suke bautawa, ton ku zo mana da huja mabayyaniya, sai manzannin suka ce musu lalle mu mutane ne irin ku sai dai Allah yana ni’ma ga wanda ya so a ciki bayin sa, ba mu iya zuwa muku da wata hujja sai da izinin Allah”*. Suratu Ibrahim, aya ta:10-11.

## - IMANI DA RANAR KARSHE.

Ranar karshe: (Ranar tsayuwa ita ce wadda za'a tayar da mutane a cikin ta domin gididdiga da sakamako) An kira ta haka ne saboda babu wani yini a bayanta. Lokacin ne 'yan aljannah za su tabbata a masaukin su haka 'yan wuta.

**Imani da ranar kiyama ya kunshi abubuwa hudu:**

1. Imani da tayar da mutane: kuma shi ne rayar da matattu lokacin da za'a yi busa ta biyu, sai mutane su tsayu gaban Ubangijin su huntaye marasa takalma, tsirara mara sa

sutura masu labba babu kaciya Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿كَمَا بَدَأْنَآ أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُۥۚ وَعْدًا عَلَيْنَآۚ إِنَّا كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٠٤﴾ الأنبياء: ١٠٤

**Ma'ana:** *"Kamar yadda muka fara halitta zama maida ta, wannan alkawari ne akan mu, lalle mu mun kasancce masu aikatawa"*. Suratul Anbiya, aya ta:104.

Kuma tayar da mutum bayan ya mutu:- Gaskiya ne tabbatacce ne a Alkur'ani da Hadisi, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ثُمَّ إِنَّكُم بَعْدَ ذَٰلِكَ لَمَيِّتُونَ ١٥ ثُمَّ إِنَّكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ تُبْعَثُونَ ١٦﴾ المؤمنون: ١٥ - ١٦

“Sannan ku bayan haka zaku mutu, sa’annan ranar kiyam a tashe ku”.

Annabi (Tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi) ya ce: *“Za’a tada mutane ranar kiya huntaye tsirara”.* (Buhari da Muslim).

Musulmai sun hadu akan tabbatar da haka, kuma shi Allah mai zartar da hukunci ne ta yadda ya zaratar da aiko manzanni kuma ya sanya wa mutane lokaci (iyaka) domin a saka musu akan abinda aka dora musu ta harsunan manzanni, Allah ta’ala ya ce:

﴿ أَفَحَسِبْتُمْ أَنَّمَا خَلَقْنَاكُمْ عَبَثًا وَأَنَّكُمْ إِلَيْنَا لَا تُرْجَعُونَ ١١٥ ﴾
المؤمنون: ١١٥

**Ma'ana:** *“Shin kuna zaton an halicce ku don wasane kuma lalle ku ba za ku koma zuwa*

*gare mu ba?.* Suratul Mu'uminun, aya ta: 115.

Kuma ya ce wa Annabin sa ﷺ:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِى فَرَضَ عَلَيْكَ ٱلْقُرْءَانَ لَرَآدُّكَ إِلَىٰ مَعَادٍ ﴾
القصص: ٨٥

**Ma'ana:** *“Lalle wadannan da ya saukar maka da AlKur’ani tabbas mai dawo da kai ne zuwa ranar sakamako”*. Suratul Kasas, aya ta:85.

1. Imani da gididiga da kuma sakamako: Za’a yi wa bawa hisabi akan ayyukan sa, kuma a sakamasa, AlKur’ani da hadisi da ijma'in musulmi sun tabbatar da haka. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ إِنَّ إِلَيْنَآ إِيَابَهُمْ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا حِسَابَهُم ﴿٢٦﴾ ﴾ الغاشية: ٢٥ - ٢٦

**Ma'ana:** "Lalle komawarr su na gare mu, kuma hisabinsu na kammu". Suratul Ghashiya, aya ta: 25-26. Kuma ya ce:

﴿ مَن جَآءَ بِٱلْحَسَنَةِ فَلَهُۥ عَشْرُ أَمْثَالِهَا ۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا يُجْزَىٰٓ إِلَّا مِثْلَهَا وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿١٦٠﴾ ﴾ الأنعام: ١٦٠

**Ma'ana:** *"Duk wanda ya zo da abu mai kyau yana da lada goma misalin shi, kuma wanda ya zo da mummuna ba shi da sakamako sai misalinsa, kuma su ba za'a zalunce su ba"*. Suratul An'am, aya ta:160. Kuma ya ce:

﴿ وَنَضَعُ ٱلْمَوَٰزِينَ ٱلْقِسْطَ لِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ فَلَا تُظْلَمُ نَفْسٌ شَيْـًٔا ۖ وَإِن كَانَ مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ أَتَيْنَا بِهَا ۗ وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ٤٧ ﴾ الأنبياء: ٤٧

**Ma'ana:** *“Za mu ajiye mizani (ma'auni) mai adalci a ranar kiyama, saboda haka ba za’a zalunce kowacce rai ba ta da komai ba, ko da ya kasance nauyin kwayar zarra ce na laifi za mu zo da shi. Kuma ya isa cewar mune masu hisabi".* Anbiya,aya ta:47.

Daga da Umar Allah ya kara masa yarda, lalle Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce: *“Allah yana kusantar da mumini sai ya dora masa sutararsa ya sturcceshi da ita , sai ya ce: Kasan zunubi kaza? Kasan zunubi kaza?*

*Bawa sai ya ce: Eh! Har ya tabbatar da haka bawan sai ya ga cewa ya halaka, sai Allah ya ce; na suturttaka a duniya, yau kuma ni na gafarta maka, sai a ba shi littafin kyawawan ayyukanshi. Amma shi kafiri da munafiki Allah zai kira su a gaban kowa, ya ce: wadannan sune suka yi wa Allah karyata, saboda haka la'anta ta tabbata ga azzalumai"*. (Buhari da Muslim).

Ya tabbata daga Annabi ﷺ cewa lalle wanda ya kudurta aikata kyakkyawan aiki kuma ya aikata to za'a rubuta masa lada goma har a cikan masa zuwa dari bakwai zuwa kuma ninkin-ba-ninkin, kuma idan ya

kudurta mummuna, kuma ya aikata za'a rubuta masa laifi daya".

Musulmi sun hadu akan tabbatar da gididiga da hisabi akan ayyuka, akan haka ne Allah ya saukar da littafi kuma ya aiko da manzanni kuma ya lazimta wa mutane karban abin da suka zo da shi da kuma aiki da abin da ya zama wajibi akansu na daga littafi, kuma ya wajabta a yaki wadanda suka ki bin abin da suka kawo, kuma ya halatta jinin su da 'ya'yansu da matan su da dukiyar su. Dabadun ya kasance akwai hisabi ba, da haka ya kasance abun tsarkake gare su daga Ubangiji mai hikima. Hakika Allah ya yi ishara da fadin cewa:

﴿ فَلَنَسْـَٔلَنَّ ٱلَّذِينَ أُرْسِلَ إِلَيْهِمْ وَلَنَسْـَٔلَنَّ ٱلْمُرْسَلِينَ ۝٦ فَلَنَقُصَّنَّ عَلَيْهِم بِعِلْمٍ ۖ وَمَا كُنَّا غَآئِبِينَ ۝٧ ﴾ الأعراف: ٦ - ٧

**Ma'ana:** *"Kuma wallahi sai mun tambayi wadanda muka aika musu kuma sai mun tambayi wadanda wadanda muka aika (manzanni Kenan) kuma za mu ba su labari da ilimi kuma bamu kasance masu boyuwa ba*"?. A'araf, aya ta:6-7.

2. Imani da aljannah da wuta:- Tare da cewa za'a cika su da halitta har abada. Aljannah (gidan ni'ima ce wacce Allah ya tanadeta ga muminai masu kiyaye dokokin sa kuma sune wadanda suka yi imani da abinda Allah ya wajabta mauu shi, kuma suka tsayu don yi wa Allah da manzon sa biyayya, masu

tsarkake wa ne ga Allah masu bin manzonsa. Akwai ni’ma a ciki irin wadda ido bai taba gani ba, kunne bai taba ji ba, zuciyar mutum ba taba hararo masa yadda take ba”. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ أُو۟لَـٰٓئِكَ هُمْ خَيْرُ ٱلْبَرِيَّةِ ﴿٧﴾
جَزَآؤُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّـٰتُ عَدْنٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَـٰرُ خَـٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ
رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِىَ رَبَّهُۥ ﴿٨﴾ ﴾ البينة: ٧ - ٨

**Ma'ana:** *“Lalle wadanda suka yi imani kuma suka yi aike nakwarai sune mafi alherin halittu. Zakamakon su a wurin Ubangijinsu shi ne aljannah wacce koramu ke gudana a karkashita suna masu dawwama a cikinta har abada Allah ya yarda da su kuma sun yarda da shi wannan sakamakon na dukkan*

IslamHouse.com

*wanda ya ji tsoron Ubangijin sa ne”*. Suratul Bayyina, aya ta:7-8. Kuma Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ فَلَا تَعۡلَمُ نَفۡسٞ مَّآ أُخۡفِيَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعۡيُنٖ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٧ ﴾ السجدة: ١٧

**Ma'ana:** *Kuma rai ba ta san abinda aka boye musu ba na abindake aranta rai, kuma sakamako ne na abinda suka kasance suna aikatawa"*. Sajada, aya ta:17.

Amma wuta (itace gidan azaba wacce Allah ya tanadar da ita ga kafirai masu zalunci wadanda suka sabawa Allah da manzon sa. A cikin ta akwai nau’in azaba daban-daban

wacce ba'a taba tunaninta ba. Allah ta’ala ya ce:

﴿ فَٱتَّقُواْ ٱلنَّارَ ٱلَّتِي وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُۖ أُعِدَّتۡ لِلۡكَٰفِرِينَ ٢٤ ﴾ البقرة: ٢٤

**Ma'ana:**“To ku ji tsoron wuta wacce aka tanadar da ita ga kafirai”. Kuma ya ce:

﴿ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمۡ سُرَادِقُهَاۚ وَإِن يَسۡتَغِيثُواْ يُغَاثُواْ بِمَآءٖ كَٱلۡمُهۡلِ يَشۡوِي ٱلۡوُجُوهَۚ بِئۡسَ ٱلشَّرَابُ وَسَآءَتۡ مُرۡتَفَقًا ٢٩ ﴾ الكهف: ٢٩

**Ma'ana:** *“Lalle mu mun tanada wa azzalumai wuta wacce ta kewaye su tana babbaka su, kuma in sun nemi agaji sai a basu agaji da ruwa mai kune fuska, tir da abun da suka sha kuma abun da suka*

*kwankwada ya munana"*. Kahf, aya ta:29.

Kuma ya ce:

﴿ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ لَّا يَجِدُونَ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ٦٥ يَوۡمَ تُقَلَّبُ وُجُوهُهُمۡ فِي ٱلنَّارِ يَقُولُونَ يَٰلَيۡتَنَآ أَطَعۡنَا ٱللَّهَ وَأَطَعۡنَا ٱلرَّسُولَا۠ ٦٦ وَقَالُواْ رَبَّنَآ إِنَّآ أَطَعۡنَا سَادَتَنَا وَكُبَرَآءَنَا فَأَضَلُّونَا ٱلسَّبِيلَا۠ ٦٧ ﴾
الأحزاب: ٦٥ - ٦٧

**Ma'ana:** *Allah ya la'anci kafirai kuma ya tanada musu wutar sai'ra, suna masu dawwama a cikin ta har abada, ba za su samu matimako ko maji'banta ba, a ranar da za'a juya fuskokin su a wuta suna cewa; inamadai mun yi biyayya ga Allah da manzansa"*. Ahzab, aya ta:65-67.

Kuma Imani da ranar karshe ya kunshi Imani da duk abinda ya kasance bayan mutuwa.

Misali: **(a) Fitinar kabari:** Ita ce tambayar mamaci game da Ubangijinsa da Annabinsa da Addininsa bayan an binne shi, sai Allah ya datar da wadanda suka yi imani da zance tabbatacce sai ya ce: Ubangiji na Allah, Addinina Musulunci ne kuma Annabi na shi ne Muhammad (Tsira da aminci su tabbata agareshi).

Sai azzalumai su bace sai ya ce. Ha! Ha! Ban sani ba, sai munafiki da wanda ya yi ridda ya ce: Ban sani ba na ji mutane suna cewa wani abu sai ni ma na fada.

**(b) Azabar kabari** da ni'ma: ita azabar kabari tana kasance wa ne ga azzalumi da kafiri da munafiki Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي غَمَرَٰتِ ٱلۡمَوۡتِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓاْ أَيۡدِيهِمۡ أَخۡرِجُوٓاْ أَنفُسَكُمُۖ ٱلۡيَوۡمَ تُجۡزَوۡنَ عَذَابَ ٱلۡهُونِ بِمَا كُنتُمۡ تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ غَيۡرَ ٱلۡحَقِّ وَكُنتُمۡ عَنۡ ءَايَٰتِهِۦ تَسۡتَكۡبِرُونَ ﴿٩٣﴾ ﴾ الأنعام: ٩٣

**Ma'ana:** *"Da zaka ga azzalumai a lokacin da suke magagin mutuwa kuma malai'ku sun baza hannun su suna cewa; ku ito da rayukanku, a ranr suna cewa ku dandani wulakantacciyar azaba na abun da kuke fada akan Allah wanda ba na gaskiya ba, kuma ku ka kasance game da ayyoyin mu masu girma kai"*. An'am, aya ta:93. Kuma Allah ya ce ga iyalen Fir'aun:

﴿ ٱلنَّارُ يُعۡرَضُونَ عَلَيۡهَا غُدُوّٗا وَعَشِيّٗاۖ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ أَدۡخِلُوٓاْ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ أَشَدَّ ٱلۡعَذَابِ ﴿٤٦﴾ ﴾ غافر: ٤٦

**Ma'ana:** *"Wuta ce za'a ta ake kawosu kantta da ita safiya da maraice, aranar kiyama kuma za'a ku shigar da mutanan Fir'auna matsananciyar azaba"*. Suratu Ghafir, aya ta:46.

A cikin Sahihu Muslim daga Hadisin Zaid bn Thabit daga Annabi ﷺ ya ce; *"Da badin kada ku binne junanku ba da na roki Allah da ya jiyar da ku azabar kabari wadda nake ji*". Sannan ya juya fuskar sa sai ya ce: *"Ku nemi tsarin Allah daga azabar wuta*". Sai muka ce Allah ya tsare mu daga azabar wuta, sai ya ce: *"Ku nemi tsarin Allah daga azabar kabari*". sai muka ce muna neman tsarin Allah daga azabar kabari. Sai ya ce: *"Ku nemi*

*tsarin Allah daga azabar abin da ya bayyana daga gareta na azaba da kuma abin da ya boyu*". Sai muka ce muna neman tsarin Allah daga abin da ya bayyan kuma da kuma wanda ya boyu. Sai ya ce: *"Ku nemi tsarin Allah daga fitinar Jujal"*. Sai suka ce: *"Muna neman tsarin Allah daga itinar Jujal".*

Amma ni'imar kabari tana tabbata ne ga mumini mai gaskiya Allah ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسۡتَقَٰمُواْ تَتَنَزَّلُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَلَّا تَخَافُواْ وَلَا تَحۡزَنُواْ وَأَبۡشِرُواْ بِٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٣٠﴾ فصلت: ٣٠

**Ma'ana:** *"Lalle wadanda suka ce Ubangijin mu shi ne Allah sannan suka tsayu a haka*

*malaiku suna sassauka a gare su suna cewa kar ku ji tsoro kar ku yi bakin ciki, ku yi bushara da aljannah wacce kuka kasance ana muku alkawarinta"*. Fussilat, aya ta:30.

Allah ya kuma ce:

﴿ فَلَوْلَآ إِذَا بَلَغَتِ ٱلْحُلْقُومَ ﴿٨٣﴾ وَأَنتُمْ حِينَئِذٍ تَنظُرُونَ ﴿٨٤﴾ وَنَحْنُ أَقْرَبُ إِلَيْهِ مِنكُمْ وَلَٰكِن لَّا تُبْصِرُونَ ﴿٨٥﴾ فَلَوْلَآ إِن كُنتُمْ غَيْرَ مَدِينِينَ ﴿٨٦﴾ تَرْجِعُونَهَآ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٨٧﴾ فَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿٨٨﴾ فَرَوْحٌ وَرَيْحَانٌ وَجَنَّتُ نَعِيمٍ ﴿٨٩﴾ ﴾ الواقعة: ٨٣ - ٨٩

**Ma'ana:** *"Kuma a lokacin da rai ta kai wuya, kuma lokacin kuna kallo, kuma mu muka fi ku kusa da shi amma ba kwa gani. To, don me in dai kun kasance ba wadanda za a yi wa sakamako ba? ku mayar da shi (cikin*

*jikinsa) in kun kasance masu gaskiya. To amma in (mai mutuwar) ya kasance daga cikin na makusanta? Sai huta da kyakkyawan abinci da Aljannar ni'ima?".* Har karshe.

An karbo daga Barra'u da Azzib Allah ya yarda da shi lalle Annabi ﷺ ya ce: "Ga muminin da ya amsa tambayar mala'iku akabarinsa: Sai mai kira ya yi daga sama cewa bawana ya yi gaskiya, saboda haka ku yi masa shimfida a Aljannah, ku tufatar da shi daga aljannah, ku bude masa kofar Aljannah. sai ya ce: sai Hututun Aljanna da kamshinta su zo masa, sai kuma a buda masa a kabarinsa iya ganinsa). Ahmad da

Abi Dawud suka ruwaito a wani dogon hadisi.

**Imani da lahira na da amfani ga mumini kamar haka:**

1. Kwadaitarwa game da aiki mai kyau da kuma kwadayin samun lada a wannan ranar.

2. Tsoratarwa ga mai aikata sabo da kuma yarda da shi saboda tsoron a zaban wannan ranar.

3. Sa ran mumini ga abin da yake kaunar samun lada a lahira.

Hakika kafirai sun musanta tashi bayan mutuwa sun riya cewa ba zai faru. Wannan abin da suka riya kuwa batacce ne a shari'ah

da da kuma a abinda muke gani haka kuma a hankalce.

Amma dalili daga shar'ance Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ زَعَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن لَّن يُبۡعَثُواْۚ قُلۡ بَلَىٰ وَرَبِّي لَتُبۡعَثُنَّ ثُمَّ لَتُنَبَّؤُنَّ بِمَا عَمِلۡتُمۡۚ وَذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٧ ﴾ التغابن: ٧

**Ma'ana:** *"Kuma kafirai sun riya riyawa cewa ba za'a taba tashinsu ba. Ka ce musu a'a ina rantsuwa da Ubangijina wallahi za'a tayar da ku, sanan a ba ku labarin da duk abin da kuka aikata yin haka ga Allah abu ne mai sauki"*. Suratut Taghabun, aya ta: 7.Hakika kuma littattafan da aka saukar daga sun yi ittifaki akan haka.

Amma gani da ido kuwa: Hakika Allah ya nuna ma bayinsa a cikin duniya yadda ya rayar da matattu, a suratul Bakara akwai misalai kuda biyar, su ne kuma:-

**Misali na daya**:- Ga mutanan Annabi Musa ﵇ lokacin da suka ce ba za mu yi Imani ba sai mun ga Allah a fili sai Allah ya kashe su sannan ya raya su, a kan hakane Allah madaukakin sarki yake cewa ga Bani Israila:

﴿ وَإِذْ قُلْتُمْ يَـٰمُوسَىٰ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ نَرَى ٱللَّهَ جَهْرَةً فَأَخَذَتْكُمُ ٱلصَّـٰعِقَةُ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿٥٥﴾ ثُمَّ بَعَثْنَـٰكُم مِّنۢ بَعْدِ مَوْتِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٥٦﴾ ﴾ البقرة: ٥٥ - ٥٦

**Ma'ana:** *"Ka tuna lokacin da kuka ce; Ya Musa! Ba za mu taba yin Imani da kai ba har*

*sai mun ga Allah a fili. Sai mutuwa ta dankeku, sannan muka tayar da ku domin ku gode”*.Bakara, ya ta:55.

**Misali na biyu:-** Game da mutumin da aka kashe a cikin Banu Israila, sai Allah ya umurce su da su yanka saniwa sai su doki mamacin zai tashi ya ba su labarin wanda ya kashe shi, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَإِذْ قَتَلْتُمْ نَفْسًا فَادَّارَأْتُمْ فِيهَا ۖ وَاللَّهُ مُخْرِجٌ مَا كُنْتُمْ تَكْتُمُونَ ﴿٧٢﴾ فَقُلْنَا اضْرِبُوهُ بِبَعْضِهَا ۚ كَذَٰلِكَ يُحْيِي اللَّهُ الْمَوْتَىٰ وَيُرِيكُمْ آيَاتِهِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٧٣﴾ ﴾ البقرة: ٧٢ - ٧٣

**Ma'ana:** *“Ku tuna lokacin da kuka yi kisan kai kuka dunga tunkudawa juna laifi a cikinsa, kuma Allah mai fitar da abinda kuka*

*kasance kuna boyewa ne"*.Bakara, aya ta:72-73.

**Misali na uku:-** Game da labarin wasu mutane da suka fita daga gidajen su don tsoron mutuwa sai Allah ya dauki rayukansu kuma ya rayar da su. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ ۞ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ خَرَجُوا۟ مِن دِيَٰرِهِمْ وَهُمْ أُلُوفٌ حَذَرَ ٱلْمَوْتِ فَقَالَ لَهُمُ ٱللَّهُ مُوتُوا۟ ثُمَّ أَحْيَٰهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٢٤٣﴾ ﴾ البقرة: ٢٤٣

**Ma'ana:** *"A she ba ka ga wadannan da suka fita daga gidajen su ba daa tsoron mutuwa sai Allah ya ce dasu; "Ku mutu" sanna ya rayar da su, lalle Allah ma'abocin falala ne*

*ga mutane, saidai mafi yawan mutane ba sa godiya"*. Bakara, aya ta: 243.

**Misali na hudu:-** Ga wanda ya gitta ta wani gari ya ga duk mutanan garin sun mutu sai ya yi mamakin yadda Allah zai rayar da su, sai Allah ya dauki ransa tsawon shekara dari sannan Allah ya rayar da shi. Da haka Allah madaukakin sarki yake cewa:

﴿ أَوْ كَٱلَّذِى مَرَّ عَلَىٰ قَرْيَةٍ وَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا قَالَ أَنَّىٰ يُحْىِۦ هَٰذِهِ ٱللَّهُ بَعْدَ مَوْتِهَا ۖ فَأَمَاتَهُ ٱللَّهُ مِاْئَةَ عَامٍ ثُمَّ بَعَثَهُۥ ۖ قَالَ كَمْ لَبِثْتَ ۖ قَالَ لَبِثْتُ يَوْمًا أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ ۖ قَالَ بَل لَّبِثْتَ مِاْئَةَ عَامٍ فَٱنظُرْ إِلَىٰ طَعَامِكَ وَشَرَابِكَ لَمْ يَتَسَنَّهْ ۖ وَٱنظُرْ إِلَىٰ حِمَارِكَ وَلِنَجْعَلَكَ ءَايَةً لِّلنَّاسِ ۖ وَٱنظُرْ إِلَى ٱلْعِظَامِ كَيْفَ نُنشِزُهَا ثُمَّ

نَكْسُوهَا لَحْمًاۚ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥ قَالَ أَعْلَمُ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٥٩﴾ البقرة: ٢٥٩

**Ma'ana:***"Ko wanda ya gitta ta wani gari a lokacin mutanan garin duk sun mutu, sai ya ce; Ta yaya Allah zai rayar da mutanan wannan gari bayan sun mutu? Sai Allah ya dauki rayuwarsa tsawon shekara dari, sannan sai ya tayar da shi, ya ce (da shi) shekara nawa ka yi? Sai (mutumin) ya ce; yini ko wani sashi na yini, sai (Allah) ya ce da shi; A'a, ka zaunane shekaru dari, kallai abincinka da abinshanka bai canza ba, kuma kallaci jakinka domin mu sanyaka darasi, kallaci kasusuwan (jakin) yadda muke tarata sannan muka lullubeshi da nama. Lokacin*

*da wannan ya bayyana a gareshi sai ya ce; ina sane lalle Allah mai iko ne akan komai"*. Suraul Bakara, aya ta:259.

**Misali na biyar:**- Game da labarin Annabi Ibrahim ﷺ lokacin da ya nemi Allah ya nuna masa yadda yake rayar da matattu? Sai Allah ya umurce shi da ya yanka tsuntsaye hudu kuma ya raba su ya dora akan dutsen da ke kusa da shi sannan ya kira ko wanne daga cikin su (su tsuntsayan). Saida ya yi haka sai gashi sun zo ga Ibrahim ﷺ suna tafiya. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِـۧمُ رَبِّ أَرِنِي كَيْفَ تُحْيِ ٱلْمَوْتَىٰ ۖ قَالَ أَوَلَمْ تُؤْمِن ۖ قَالَ بَلَىٰ وَلَـٰكِن لِّيَطْمَئِنَّ قَلْبِي ۖ قَالَ فَخُذْ أَرْبَعَةً مِّنَ ٱلطَّيْرِ فَصُرْهُنَّ

إِلَيْكَ ثُمَّ ٱجْعَلْ عَلَىٰ كُلِّ جَبَلٍ مِّنْهُنَّ جُزْءًا ثُمَّ ٱدْعُهُنَّ يَأْتِينَكَ سَعْيًا ۚ وَٱعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٦٠﴾ البقرة: ٢٦٠

**Ma'ana:** *"Ka tuna lokcin da Ibrahim ya ce; Ya Ubangiji ka nuna mini yadda kake rayar da mattace? Sai (Allah) ya ce; Shin ba ka yi Imani ba ne? sai (Annabi Ibrahim) ya ce; Na yi, saidai domin zuciyata ta dada samun natsuwa, sai (Allah) ya ce (masa); ka kama tsuntsaye hudu, kuma ka daddatsa su, sannan ka sanya kowanne kaso akan dutse, sannan ka kira su, za su zo maka suna tafiya, ka sani lalle Allah mabuwayi ne mai hikima*. Suratul Bakara, aya ta:260.

Wadannan su ne misalai da kowa ya tabbatar, sun kuma nuna lalle za'a rayar da

matattu. Hakika ishara ta gabata ga abubuwan da Allah ya bai wa Annabi Isah dan Nana Maryam ﷺ wajan rayar da matattu da kuma fitar da su daga kabari da izinin Allah.

Amma dalilin hankali ya tabbatar da shi yana da fuskoki biyu:

**Na farko:-** Lalle Allah ne ya kirkiri halitar sammai da kassai da abun da ke cikin su, kuma mai ikon ya fara halittu ai kuwa ba zai gagare shi ba wajen dawo da su ba, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَهُوَ ٱلَّذِي يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهۡوَنُ عَلَيۡهِ ﴾ الروم: ٢٧

**Ma'ana:** *"Kuma shi ne wanda ya fara halitta sannan ya mai da ta kuma maidawar ma shi ya fi sauki a gareshi"*. Suratur Rum, aya ta:27. Kuma ya ce:

﴿كَمَا بَدَأْنَآ أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُۥ ۚ وَعْدًا عَلَيْنَآ ۚ إِنَّا كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٠٤﴾ الأنبياء: ١٠٤

**Ma'ana:** *"Kamar yadda muka fara hlitta za mu mai da ta, wannan alkawari ne akan mu, lalle mu mun kasance masu aikatawa."* Anbiya, aya ta: 104. Kuma ya ce a matsayin raddi ga masu musanta tashi bayan mutuwa, Allah ya ce:

﴿قُلْ يُحْيِيهَا ٱلَّذِىٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٍ ۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلْقٍ عَلِيمٌ ٧٩﴾ يس: ٧٩

**Ma'ana:** *"Ka ce mai raya su, shi ne wanda ya samar da su tun a karon farko, kuma shi masani ne ga dukkanin halitta"*. Suratu Yasin, aya ta:79.

**Na biyu:-** Lalle kasa ta kasance matacciya ashinfide, babu itatuwa koraye, sai ruwa ya sauka akan su, sai ta taso ta zamo tsanwa rayayyiya bayan ta mace, daga nan sai ta tsirar da nau'ukan tsirrai masu ban sha'awa, kuma shi mai ikon rayar da su bayan mutuwa. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنَّكَ تَرَى ٱلْأَرْضَ خَٰشِعَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا ٱلْمَآءَ ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ ۚ إِنَّ ٱلَّذِىٓ أَحْيَاهَا لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ٣٩ ﴾

فصلت: ٣٩

**Ma'ana:** “Kuma akwi daga cikin ayoyinsa shi ne lalle kai kana gaanin kasa ta bushe to idan muka saukar mata da ruwa sai ta girgiza ta habbaka, lalle wanda ya rayata hakika mai raya matattu ne, lalle shi mai iko ne akan komai. Fussilat, aya ta:39.

Kuma ya ce:

﴿ وَنَزَّلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً مُّبَٰرَكًا فَأَنۢبَتْنَا بِهِۦ جَنَّٰتٍ وَحَبَّ ٱلْحَصِيدِ ﴿٩﴾ وَٱلنَّخْلَ بَاسِقَٰتٍ لَّهَا طَلْعٌ نَّضِيدٌ ﴿١٠﴾ رِّزْقًا لِّلْعِبَادِ ۖ وَأَحْيَيْنَا بِهِۦ بَلْدَةً مَّيْتًا ۚ كَذَٰلِكَ ٱلْخُرُوجُ ﴿١١﴾ ﴾ ق: ٩ - ١١

**Ma'ana:** *"Kuma mau saukar da ruwa daga sama mai albarka sai muka fitar da shi gonaki, da kwaya abar girbewa, da itan dabino dogaye suna da 'ya'yan it ace gunda*

*masu hauhawar juna. Don arziki ga bayi, kuma muka rayar da da shi (ruwan) kasa da ta bushe, kamar wannan ne fita daga kabari take"*. Surat K, aya ta:9:11.

Hakika karkatattu sun musanta azabar kabri da ni'marsa, suna cewa ba zai faru ba, sukace da za'a bude kabarin mamaci da za'a same shi kamar yadda yake, kuma kabari ba ya karawa ko ragewa.

Wannan riwaya da suke yi karya ce da dalilin Shari'ah da abinda aka gani da kuma na hankali duk sun yi watsi da maganar su.

Dalilin Shari'ah kuwa:- Hakika nassoshi sun gabata a wannan rubutn da muka yi game

da wanda ya yi Imani da lahira, za samu bayanin a can.

A cikin Sahihil Buhari daga Hadisin Dan Abbas Allah ya kara musu yarda ya ce: *"Annabi ﷺ ya fita wajan katangun madina sai ya ji ihun wasu mutane biyu ana musu azaba a kabarinsu"* sai ya bada labarin hakan, a cikin labarin yana cewa: *"Amma dayansu ya kasance ba ya suturcewa daga fitsari"*. A wata ruwayar kuma: *"Daga fitsarinsa, dayan kuma ya kasance yana yawo da gulma"*.

Dalilin abunda aka gani kuwa: Mai bacci yana gani a cikin baccin sa yana wuri mai girma ana shakatawa a cikin sa ko yana wuri

mai matsi ya matsu, saudayawa zai iya tashi wani lokaccin bai manta abin da ya gani ba, a dudda haka kuma yana tabarmarsa a gadon dakinsa, bacci dan'uwan mutuwa ne da haka Allah ya kira shi da mutuwa. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ ٱللَّهُ يَتَوَفَّى ٱلۡأَنفُسَ حِينَ مَوۡتِهَا وَٱلَّتِي لَمۡ تَمُتۡ فِي مَنَامِهَاۖ فَيُمۡسِكُ ٱلَّتِي قَضَىٰ عَلَيۡهَا ٱلۡمَوۡتَ وَيُرۡسِلُ ٱلۡأُخۡرَىٰٓ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّى ﴾ الزمر: ٤٢

**Ma'ana:** *"Allah shi ne ya kashe rayuka lokacin mutuwar su da wacce kuma ba ta mutuba a cikin baccinta sai ya rike wacce aka hukunta mata mutuwa, sai kuma ya sako dayar (wacce lokacin mutuwarta bai yi*

*ba) zuwa wani lokaci sananne"*. Suratuz Zumar, aya ta:42.

**Dalilin hankali kuwa:**- mai bacci yana gani a mafarki kuma ya tabbata da gaske maarkin ma ya yi daidai da abinda yake a zahiri, wani lokacin ma ya ga Annabi ﷺ a sifarsa, kuma dukkan wanda ya ganshi a siffarsa tabbas shi ya gani, tare da haka mai bacci yana cikin dakinsa akan shinida nesa ma da abinda ya gani, to idan wannan ya zamo abu ne maiyiwuwa a duniyance to shi ne kuma ba zai iya yuwuwa ba a lahira?.

Amma abinda suka dogara da shi cewa da za'a bude kabari da za'a same shi kamar yadda yake, kuma kabari ba ya canzawa

wajan fadi ko ya rage ga amsa gare su kamar haka:-

**Na daya:-** Lalle shi baya halatta a juya wa abin da Shri'ah ta zo da shi baya, kamar misalin wannan shubuhar batacciya wacce idan aka lura da ita abin da shari'ah ta zo da shi matuka da sun san wannan batanciyar shubuhar. Masu hikima sun ce:  Sau nawa wanda yake aibanta kyakkyawar Magana, ashe hakan ya zo ne ta a rashin kyakkyawar mahimta da yake da ita.

**Na biyu:**- Hali na rayuwar kabari lamari ne na boye wanda gababuwa basa iya gani, da zai kasance mutane na gani ne, to imani da gaibi da muminai suka yi zai zama ba

banbanci da karyatawar da wadanda suka ki gasgatawa suka yi.

**Na uku:-** Lalle azaba da ni'mar kabari da matsi da fadin kabarin mamaci ne kawai yake gani ban da wanin sa. Kamar yadda mai bacci shi kadai yake ganin wurin da yake matsatse ko a fili, wanna yana faruwa ne gare shi kadai. Hakika manzon Allah ﷺ ana masa wahyi a lokacin yana tsakiyar sahabban sa, amma ba wanda yake jin abinda ake yi wa Ma'aikin Allah ﷺ na wahayi, wani lokacin kuma mala'ika yana yana canza siffa sai ya yi Magana da Ma'aikin Allah ﷺ, amma kuma ba za su ganshi ba kuma ba za su ji shi ba.

**Na hudu:-** Jin mutane kayyadajje ne akan abin da Allah ya iyakance musu, bai kamata su ji komai da komai ba. Sammai da kasa da aibndake cikin su suna yi wa Allah tasbihi, Allah na jiyar da wanda ya ga dama daga halittunsa kuma an katange wasu daga daga cikin mu. Da haka ne ya ce:

﴿ تُسَبِّحُ لَهُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ ٱلسَّبۡعُ وَٱلۡأَرۡضُ وَمَن فِيهِنَّۚ وَإِن مِّن شَيۡءٍ إِلَّا يُسَبِّحُ بِحَمۡدِهِۦ وَلَٰكِن لَّا تَفۡقَهُونَ تَسۡبِيحَهُمۡ ﴾الإسراء: ٤٤

**Ma'ana:** *"Abin dake cikin sammai da kassai da abin da ke tsakanin su, suna tasbihi ga Allah, babu wani abu face sai yana tasbihi da godiya ga Allah, amma ku baku fahimtar tasbihin na su."* Suratul Isra'i, aya ta: 44. Haka ma shaidanu da aljanu suna kai-komo,

kuma ya tabbata aljanu zo wurin manzon Allah ﷺ suna sauraron karatun Alkur'ani suka saurari karatunsa suka kuma yi shiru, suka koma wurin jama'arsu suna musu gargadi tare da haka muka fahimci wadanda aka katange mu daga gare su. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ لَا يَفۡتِنَنَّكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ كَمَآ أَخۡرَجَ أَبَوَيۡكُم مِّنَ ٱلۡجَنَّةِ يَنزِعُ عَنۡهُمَا لِبَاسَهُمَا لِيُرِيَهُمَا سَوۡءَٰتِهِمَآۚ إِنَّهُۥ يَرَىٰكُمۡ هُوَ وَقَبِيلُهُۥ مِنۡ حَيۡثُ لَا تَرَوۡنَهُمۡۗ إِنَّا جَعَلۡنَا ٱلشَّيَٰطِينَ أَوۡلِيَآءَ لِلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ ٢٧ ﴾ الأعراف: ٢٧

**Ma'ana:** *"Ya ku yan Adam kar shaidan ya fitine ku kamar yadda ya fitar da babanku daga Aljannah ya cire musu tufafin su domin ya nuna musu tsiraicinsu, lalle (shi shaidan) yana ganinku shi da jama'arsa ta inda ba*

*kwaganinsu, lalle mu munsanya shaidanu su zama waliyyai ga wadanda ba sa yin Imani ba"*. A'araf, aya ta:27.

Idan halitta ba sa iya ganin kowa, bai kamata su musanta abin da ya tabbata na lamarin gaibi ko da ba sa ganin sa ba.

## - IMANI DA KADDRA.

Akadara da wasalin fatha a dalun (gudanar da ayyukan Allah ga halitunsa ta yadda

iliminsa ya gabata kuma ya zartar da hikmarsa).

**Imani da kaddara ya kunshi abubuwa hudu:**

1. Imani da cewa Allah yana sane da dukkan kome a dunkule da kuma a rarrabe, tun fil azal har abada ya kasance yana sane da kuma bayinsa.

2. Imani da cewa Allah ya rubuta su a lauhul mahfuz. A wannan lamura biyu Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ إِنَّ ذَٰلِكَ فِى كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٧٠﴾﴾ الحج: ٧٠

**Ma'ana:** *“A she ba ku sani ba Allah yana sane da duk abin da ke sama da kasa kuma lalle hayan rubuce a littafi kuma hakan ga Allah abu ne mai sauki?"*. Suratul Hajj, aya ta:70.

Kuma a cikin Sahihu Muslim daga Abdullahi dan Amru dan Asin Allah ya kara musu yarda ya ce:

"Na ji Manzon Allah ﷺ ya ce: “Allah ya rubuta kaddarar kowacce halitta tun kafin ya halicci sammai da kassai da shekaru dubu hamsin”.

3. Imani da cewa lalle dukkanin halittu ba sa kasance wa saida ganin damar Allah ta’ala

akan wanda ke da alaka da ayyukan sa ko na halitunsa. Allah madaukakin sarki ya ce game da ayyukansa:

﴿ وَرَبُّكَ يَخْلُقُ مَا يَشَاءُ وَيَخْتَارُ ﴾القصص: ٦٨

**Ma'ana:** *"Kuma Ubangijinka yana halittar abin da ya so kuma yana zaban wanda ya so"*. Suratul Kasas, aya ta:68. Kuma ya ce:

﴿ وَيَفْعَلُ اللَّهُ مَا يَشَاءُ ۝٢٧ ﴾ إبراهيم: ٢٧

**Ma'ana:** "Kuma Allah yana aikata abinda ya ga dama". Suratu Ibrahim, aya ta: 27. Kuma ya ce:

﴿ هُوَ الَّذِي يُصَوِّرُكُمْ فِي الْأَرْحَامِ كَيْفَ يَشَاءُ ﴾آل عمران: ٦

**Ma'ana:** *"Shi ne wannan da ke suranta ku a mahaifa yadda ya so"*. Suratu Ali Imran, aya ta: 6. Kuma ya ce game da ayyukan halittun sa:

﴿ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَسَلَّطَهُمْ عَلَيْكُمْ فَلَقَٰتَلُوكُمْ ﴾ النساء: ٩٠

**Ma'ana:** "Da Allah ya ga dama da ya dora su akan ku kuma da sun yake ku". Suratun Nisa'i, aya ta: 90. Kuma ya ce:

﴿ وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ مَا فَعَلُوهُ ۖ فَذَرْهُمْ وَمَا يَفْتَرُونَ ﴿١١٢﴾ ﴾ الأنعام: ١١٢

**Ma'ana:** *"Da Allah ya ga dama da ba su aikata ba, ka bar su da abin da suke kirkirawa"*. Suratul An'am, aya ta:1122.

4. Imani da cewa dukkanin kasantattun abubuwa halittar Allah madaukakin sarki ce da zatin su da sufofinsu da motsinsu. Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ٦٢ ﴾ الزمر: ٦٢

**Ma'ana:** *"Allah shi ne mahaliccin komai, kuma shi ne mai kulawa akan komai"*. Suratuz Zumar, aya ta:62. kuma ya ce:

﴿ وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖ فَقَدَّرَهُۥ تَقۡدِيرٗا ٢ ﴾ الفرقان: ٢

**Ma'ana:** *"Kuma ya halicci dukkan komai sai kuma ya kaddara shi kaddarawa"*. Suratul Furkan, aya ta:2. Kuma ya ce

game da maganan Annabi Ibrahim ﷺ ya ce wa mutanensa:

﴿ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمْ وَمَا تَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾ ﴾ الصافات: ٩٦

**Ma'ana:** *"Allah ne ya halicce ku da kuma abin da kuke aikatawa". "Alah ne ya halice ku da abin da kkuke aikatawa"*. Suratus Saffatt, aya ta:96.

Kuma imani da kaddara aka abin da muka siffanta ba ya kore wa bawa ikon sa akan aikin da ya zaba yake ikon akanshi, domin Shari'ah da abin da ke faruwa sun yi nuni da tabbatuwar hakan:

Amma Shari'ah: Hakika Allah ta'ala ya ce game da ganin dama:

﴿ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ مَـَٔابًا ﴿٣٩﴾ ﴾ النبأ: ٣٩

**Ma'ana:** *"Duk wanda ya ga dama ya riki hanya zuwa ga Ubangijin sa"*. Naba'i, aya ta:39. Kuma ya ce:

﴿ فَأۡتُواْ حَرۡثَكُمۡ أَنَّىٰ شِئۡتُمۡ ﴾ البقرة: ٢٢٣

**Ma'ana:** *"Ku zo wa gonakinku ta yadda kuka ga dama"*. Suratul Bakara, aya ta:223. Kuma ya ce game da Iko:

﴿ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ مَا ٱسۡتَطَعۡتُمۡ وَٱسۡمَعُواْ وَأَطِيعُواْ ﴾ التغابن: ١٦

**Ma'ana:**"Ku ji tsoron Allah gwargodon ikon ku, kuma ku ji kuma ku bi". Suratut Taghabun, aya ta: 16. Kuma ya ce:

﴿ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِلَّا وُسۡعَهَاۚ لَهَا مَا كَسَبَتۡ وَعَلَيۡهَا مَا ٱكۡتَسَبَتۡ ﴾البقرة: ٢٨٦

**Ma'ana:** *"Allah ba ya dorawa rai sai abin da za ta iya, abinda ta yi nakwarai tana da ladanshi, wanna kuma ta yin a laifi tana da zunubinsa"*. Bakara, aya ta:286.

**Amma alwaki'i**: Ko wanne mutum ya san yana da ganin dama da kuma iko, wacce yake aiki da ita, kuma hakan yana banbanta, abin da ya faru da nufinsa kamar tafiya da kuma abin da ke faruwa ba tare da nufin sa ba kamar motsin hannu lokacin tafiya, amma ganin damar bawa da ikonsa sun kasance ne da ganin damar Allah ta'ala, da

kuma ikonsa. Domin Allah madaukakin sarki ya ce;

﴿لِمَن شَآءَ مِنكُمۡ أَن يَسۡتَقِيمَ ٢٨ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٩﴾ التكوير: ٢٨ - ٢٩

**Ma'ana:** *"Ga duk wanda ya so cikin ku sai ya bi mikakkiyar hanya. Kuma ba kwa ganin damar wani sai idan Allah Ubangijin talikai ya so"*. Suratu Tak'weer, aya ta:28-29. Kuma kasancewar komai mallakar Allah ne, babu wani abin da zai kasance a mulkin sa face da saninsa da kuma ganin damar sa.

Kuma Imani da kaddara akan yadda muka siffanta ba ya ba bawa damar kafa hujja wajan barin aikata wajibai ko sabo, don

haka hujjojin sa battatu ne ta fuskoki kamar haka:

**1. Fadin Allah madaukakin sarki:-**

﴿ سَيَقُولُ ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ لَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشۡرَكۡنَا وَلَآ ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمۡنَا مِن شَيۡءٖۚ كَذَٰلِكَ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ حَتَّىٰ ذَاقُواْ بَأۡسَنَاۗ قُلۡ هَلۡ عِندَكُم مِّنۡ عِلۡمٖ فَتُخۡرِجُوهُ لَنَآۖ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَإِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا تَخۡرُصُونَ ١٤٨ ﴾ الأنعام: ١٤٨

**Ma'ana:** *"Da sannu wadanda su yi shirka za su ce; Da Allah ya so da ba mu yi shirka ba, haka iyayen mu haka kuma da ba mu haramta wani abu ba. Da haka ne wadanda suka kasance kafin su muka dandana musu azabar mu. Ko kuna da wani ilimi ku fito mana da shi?. Ba abinda da suke bi saidai*

*zato, ku kuma bakwa cikin komai sai*...". Suratul An'am, aya ta: 148. Da ace suna da hujja game da kaddara ai da allah bai dandana musu azabar sa ba.

**2. Fadin Allah madaukakin sarki:-**

﴿ رُّسُلًا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿١٦٥﴾ ﴾ النساء: ١٦٥

**Ma'ana:** *"Manzannine masu bushara kuma masu gargadi, domin kar ya kasance akwai wata hujja da mutane za su bada bayan an aiko da manzanni, kuma Allah ya kasance mabuwayi mai hikima"*. Suratun Nisai, aya ta: 165. Da kafa hujja da kaddara yana zama

dalilin wadanda suka saba, to ai da hakan bai gushe ba dudda an aiko manzannin.

3. Abin da Imam Bukhari da Muslim suka ruwaito daga Aliyu bin Abi Talib (Allah ya kara mishi yarda) lalle Annabi (ﷺ ya ce: “Babu wani daya daga cikin ku face an rubuta mazauninsa a wuta ko a Aljanna, sai wani mutum daga cikin sahabbai ya ce; Ya Ma'aikin Allah ba za mu dogara akan haka ba? Sai (Ma'aikin Allah ﷺ) ya ce: A’a! Ku yi aiki, domin kowa an sawwake masa, sannan sai ya karanta:

﴿ فَأَمَّا مَنۡ أَعۡطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ٥ ﴾ الليل: ٥

**Ma'ana:** "*To fa! Duk wanda ya bada sadaka kuma ya ji tsoron Allah”*. Suratul Lail, aya ta: 5. Kuma a wani lafazi na Muslim ya ce: *“(Kowannen ku an sawwake mishi game da duk abin da aka halicce shi domin sa)*. Sai Annabi ﷺ ya yi umurni da ayi aiki, ya hana da a dogara akan kaddara.

4. Lalle Allah ta’ala ya yi umarni ga bawa kuma ya yi hani gare shi, kuma bai tilasta masa ba sai ga abin da yake da ikon yi. Allah madaukakin sarki ya ce: *“To Ku ji tsoron Allah gwargodon ikonku”*. kuma ya ce; *"Ba’a dorawa wata rai sai abin da zata iya"*. Da bawa zai kasance wanda aka tilasta masa akan ya aikata aiki to da ai an dora masa

abinda ya fi karfinsa, wannan ko ba daidai bane, saboda haka da za'a ai kata laifi ta hanyar hajilci, ko mantuwa ko tilastawa to da ba wani laifi, domin yana da uzuri.

5. Lalle ita kaddara sirrin Allah ce wanda take rufaffa ba'a saninta sai bayan abinda aka kaddara ya auku, kuma nufin da bawa yake da shi na abinda zai aikata ta riga yi aikin na shi, sai ya kasance abinda yake so shi ne aikin da zai yi ba tare da shi ya san me Allah ya kaddara ba. To a wannan lokacin sai hujjar da zai kafa da kaddara ta kau, domin mutum ba shi da wata hujja cikin abinda ba shi da masaniya a kai.

3. Lalle mu muna ganin mutum yana kodayin aikata abin za'a zarge shi na lamarin duniyarsa har ya same shi kuma ba zai iyi kauce masa ba domin ya yi wand aba za'a zargeshi ba, sannan ya kafawa abokin adawarsa hujja da kaddara, to me yasa yake barin abinda zai anfane shi a al'amuran addininsa ya aikata abin da zai ccutar da shi, sannan ya kafa hujja (wato ya ce haka Allah ya) kaddara? A she wannan al'amaran biyu ba hukuncinsu guda ba.?

Ga misali da zai bayyana maka haka: In akwai hanyoyi biyu wacce bawa ya sani, daya tana kaiwa ga gari amma gaba-dayanta

rudu ce, ana kisa ana kwace kayayyaki ana ciwa mutane mutunci, ga tsoro ga yunwa. Ta biyu kuma hanyar tana kai wa zuwa gari mai tsari da amince, rayuwa mai dadi, kiyaye dukiya da mutuncin jama'a da sauran su to wace hanya ce mutum zai bi?.

Lalle shi zai bi hanya ta biyuce wacce za ta kai shi ga gari mai aminci. Bai kamata ga mai hankali ya bi hanyar da za ta kai shi garin da babu natsuwaba sannan kuma ya kafa hujja da kaddara (wato ya ce ai haka Allah ya kaddara) kuma mai yasa yake bin hanyar wuta banda ta Aljannah sanna ya kafa hujja da kaddara?.

Amma misali na biyu: Muna ganin mara lafiya ana umartar shi da shan magani, sai kuma ya sha dudda ransa bai so, kuma sai a hana shi cin abinda zai cutar da shi dudda ranshi yana so sai kuma ya barshi, duk yana haka ne don neman lafiya da aminci, kuma ba zai yi wu ya hana kansa shan magani ba ko ya ci abin da zai cutar da shi ba sannan ya kafa hujja da kaddara akan haka. To me yasa mutum zai bar abin da Allah da Manzanshi suka umarce shi da yi, kuma ya aikata bin da Allah ya hane shi sai kuma ya kafa hujja da kaddara?.

5. Lalle duk mai kaffa hujja da kaddara akan barin abin da yake ya wajabta ko ya aikata

laifi, to da wani mutum zai yi mishi ta'addanci ya kwace masa dukiya ko ya keta masa alfarma, sanan ya kafa masa hujja da kaddara, ya ce kar ka zarge ni domin, wuce iyakar da na yi maka haka Allah kaddara, to wanna ba zai karbi hujjar sa ba. Me yasa ba'a karbar hujja da kaddara akan abin da aka wuce iyaka akan sa, kuma ya kafama kansa hujja da wuce iyaka akan ta'addaccin da ya yin a hakkin Allah ta'ala?.

Kuma ka ana ruwaitowa daga sarkin muminai Umar bin Katab Sarkin an kawo mi shi wani barawo sai ya umurci a yanke masa hannu sai (barawon) ya ce: Ina da Magana satar da na yi akan kaddarar Allah ne, sai

Umar ﷺ ya ce masa kuma mu za mu yanke maka hannu ne da kaddarar Allah.

**Immani da kaddara yana da amfani kamar haka:**

1. Dogaro ga Allah ta'ala ta wajan aikata sabuba ta yadada mutum ba zai dogara akan sahabi ba, domin komai yana kasancewa ne da ikon Allah.

2. Kar mutum ya ji mamakin kansa a wajan samuwar abinda ya nufata, domin kaiwa ga ni'mar Allah daga Allah ne tare da kaddara shi da sababin alheri da nasara, kuma ya ji mamakin kansa yana sa shi mancewa da godiya ga ni'mar Allah.

3. Natsuwa da samur walwalar zuciya na abin da yake gudana na kaddarawar Allah,

kuma ba ya damuwa da abin da ya kubuce masa, ba kuma ya bakin ciki na wanin abun damuwa da ya same shi, domin haka na faruwa ne da ikon Allah wanda mallakar sammai take a hanunsa, kuma shi ne mai sa komai ya kasance, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مِّن قَبۡلِ أَن نَّبۡرَأَهَآۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٢٢ لِّكَيۡلَا تَأۡسَوۡاْ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمۡ وَلَا تَفۡرَحُواْ بِمَآ ءَاتَىٰكُمۡۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخۡتَالٖ فَخُورٍ ٢٣ ﴾ الحديد: ٢٢ - ٢٣

**Ma'ana**: *“Ba wata masifa da za ta samu a bayan kasa ko a kawunanku face tana cikin litafin tun kafin mu halicceta, lalle hakan a*

*wurin Allah abu ne mai sauki. Domin kada ku yi bakin ciki akan abinda ya kubuce muku, kada kuma ku farin-ciki akan abinda y aba ku. Kuma Allah ba ya son mai takama mai alahari"*. Suratul Hadid, aya ta: 22-23.

Annabi ﷺ yana cewa: "Lamari mumini abin burge wane, lalle lamarin sa alheri ne baki-daya, kuma ba mai samun haka sai mumini, ida farin ciki ya same shi ya gode wa Allah, sai ya zama alheri a gare shi, idan kuma damuwa ta same shi sai ya yi hakuri, sai zama alheri gare shi". (Muslim).

**- Hakika bangarori biyu sun bace game da abinda ya shafi kaddara.**

**Na farko** (Jabariyya) sune suka ce lalle bawa ana dora masa aiki ne ba shi da wani iko ko nufi a ikan haka.

**Na biyu** (kaddariyya) sune suka ce lalle bawa yana dauke da nufin sa da kuma iko, kuma ganin damar Allah ba shi da tasiri akan sa.

Kuma martani akan bangare na arko wato Jabariyya ta bangaren Shri'ah da kuma abin da ke faruwa: Lalle Allah ta'ala ya tabbatar wa bawan sa nufi da ganin-dama, kuma ya

jingina ayyukan gare shi. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ مِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلدُّنۡيَا وَمِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلۡأٓخِرَةَ ﴾ آل عمران: ١٥٢

**Ma'ana:** *"Daga cikin ku akwai wanda yake nufin duniya, kuma daga cikin ku akwai wanda yake nufin lahira"*. Suratu Ali Imrana, aya ta: 152. Kuma ya ce:

﴿ وَقُلِ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكُمۡۖ فَمَن شَآءَ فَلۡيُؤۡمِن وَمَن شَآءَ فَلۡيَكۡفُرۡۚ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمۡ سُرَادِقُهَا ﴾الكهف: ٢٩

**Ma'ana:** *"Ka ce; gaskiyace daga wurin Ubangijinku, duk wanda ya so ya yi Imani, kum duk wanda ya so ya kafirce, lalle mu mun tanad wa azzalumai wuta wace zata*

*zagaye su”*. Suratul Kahf, aya ta:29. Kuma ya ce:

﴿ مَّنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ٤٦ ﴾ فصلت: ٤٦

**Ma'ana:** *“Duk wanda ya aikata mai kyau to ya yi ne don kansa kuma duk wanda ya aikata mummuna to ya yi ne don kansa, kuma Ubangijinka ba mai zalincine ga bayi ba”*. Suratu Fussilat, aya ta; 46.

**Na abin da ke faruwa kuwa:** Lalle ko wane bawa ya san banbanci tsakanin irin aikin da yake yin a ganin dama, kamar nufin ci da sha da kasuwanci, da kuma irin wanda yake yi ba da san ransa ba, kamar nishi a lokacin

zazzabi da kuma fadowa daga sama, to shi bawa a na arko ya aikata don radin kansa, ba tare da wani tilasti ba. A na biyu kuwa ba da son ransa ba ne hakan ya faru.

Amma maida martini kuma ga na biyun (Kadariyya) ta bangarori biyu ne a Shari'ance da kuma a hakalce.

Amma a Shar'ance: Lalle Allah ta'ala shi ne mahaliccin dukkan komai, kuma kowanne abu yana kasance wa ne da ganin damarsa. Hakika Allah ya bayyana haka a cikin littafinsa cewa lalle ayyukan bayi suna faruwa ne da ganin damar Allah. Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلَ ٱلَّذِينَ مِنۢ بَعْدِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ وَلَٰكِنِ ٱخْتَلَفُوا۟ فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ وَمِنْهُم مَّن كَفَرَ ۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلُوا۟ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿٢٥٣﴾ ﴾ البقرة: ٢٥٣

**Ma'ana:** “Da Allah ya ga dama da wadanda ke bayansu ba su yaki juna ba bayan hujjoji sun zo musu, saidai sun saba, daga cikinsu akwai wanda ya yi Imani, kuma da Allah ya ga dama da ba su yaki junansuba, saidai Allah yana aikata abinda ya ga dama". Suratul Bakara, aya ta: 253. Kuma ya ce:

﴿ وَلَوْ شِئْنَا لَءَاتَيْنَا كُلَّ نَفْسٍ هُدَىٰهَا وَلَٰكِنْ حَقَّ ٱلْقَوْلُ مِنِّى لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ ﴿١٣﴾ ﴾ السجدة: ١٣

**Ma'ana:** *“Da mun ga dama da sai mu ba kowacce rai shiriyarta, saidai zance ya*

*tabbata tabbas sai na cika jahannama da aljanu da mutane maki-daya"*. Suratu Sajdah, aya ta;13.

**Amma game da hankali kuwa:** "Domin lalle gabadaya wannan halittar bakidayanta mallakar Allah ce, kuma mutum yana cikin wannan halittar, saboda haka shi ma mallakar Allah madaukakin sarki ne, kuma bai yi wu wa wanda ake mallaka ya yi wani tasarrufi a mulkin mai mulki saida izininsa da kuma ganin damarsa.

## - MANUFAR AKIDAR MUSULUNCI.

**'Alhadafu'** a yare: Yana hawa kan ma'an kamar haka.

Kuma manufar akidar musulunci: Manufofinta masu matukar mahimmanci suna da yawa wadanda suke kololuwarta wadanda aka umarni da a rike su sosai, daga ciki akwai.

1. Kyautata niyya da bauta domin Allah shi kadai, domin lalle shi ne mahalici ba shi da abokin taryya, saboda haka ya zama wajibi niyya da bauta ta zama ga Allah kadai.

2. 'Yantar da hankali da tunani daga barin wauta da rashin kangado wanda ke faruwa

alokacin da zuciya ba ta da wannan akidar, domin dukkan wanda zuciyarsa ta kasance babu wannan bayanan, to lalle kodai ya zama shi ba komai a zuciyarsa saboda haka yana bautar abinda yake ganine kawai. Ko kuma ya kasance yana fagabniya a akidu mara kyau wadanda suke na bata da tatsunuyoyi.

3. Samun kwanciyar hankani da natsuwa, baba wata damuwa, kuma babu wani bacin rai, domin wannan akidar tana hada bawane da mahaliccinsa, sai ya yarda da Allah shi ne Ubangiji kuma mai jujjuya al'amura, mai hukuni kuma mai shar'antawa, sai zuciyarsa ta na tsa da kaddarawar Ubangiji, kirjinsa ya

fadada da musulunci, ba zai taba neman wani canji ba.

1. Kyakkyawan niyya da kuma aiki saboda kaucewa karkata a bautawa Allah madaukakin sarki, da kuma mu'amalantar halittun Allah, domin yana cikin manyan tushen haka Imani da manzanni, wanda yake kunshe da bin hanyoyinsu wacce take tsaftatacciya ta wajan niyyah ko kuma aiki.

2. Daura damara a dukkan al'amarin da aka sag aba, ta yadda babu wata dama ta gabatar da kyakkyawa aikida zata kubuce masa, face ya ribaceta domin kwadayin ladan dake ciki, kuma ba zai taba ganin wurin laifi ba face sai ya nuisance shi domin

gudun ukuba, domin babba abin yake jagora anan shi ne Imani da za'a tashi bayan mutuwa, da kuma sakamako akan ayyuka, *"Kowadanne al'umma suna darajoji na ayyukan da suka yi, kuma Ubangijinka bai rafakana ba dangane da abinda suke aikatawa"*. Suratul An'am. Kuma hakika Ma'aikin ﷺ ya kwadaitar akan wannan babban al'amarin, a fadinsa da ya yi: *"Mumini mai karfi shi ya fi kuma shi ya fi soyuwa a wurin Allah akan mumini mai rauni, kowanne yana da alheri, ka yi kwadayi akan duk abinda zai anfaneka ka nemi taimakon Allah, kada ka gajiya. Idan wani abu ya sameka kada ka ce; Ina ma dai*

*na yi kaza da kaza!, ka ce: Haka Allah ya kaddara, kuma abinda ya ga dama ya yi, domin (inama) tana bude kofar shaidan"*. Muslim ne ya ruwaito.

1. Gina al'umma mai karfi, da zata iya bada duk wani abu tsada da mai sauki domin tabbatar da addininta, da gina turakunsa, ba tare da ta da mu ba da dukkan abinda ya sameta ba akan hakan ba, akan wannan ne Allah madaukakin sarki yake cewa:

﴿إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمْ يَرْتَابُوا۟ وَجَـٰهَدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ أُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّـٰدِقُونَ ﴿١٥﴾﴾ الحجرات: ١٥

**Ma'ana:** *"Wadanda suke muminai kawai sune wadanda suka yi Imani da Allah da kuma Manzansa sannan ba su yi kokwanto ba, kuma suka yi jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu domin daukaka addinin Allah, wannan sune ma su gaskiya"*. Suratul Hujurat, aya ta:15.

2. Kaiwa ga rabautuwa duniya da lahira. Ta hanyar gyara daidaikun mutane da kuma al'umma, da kuma neman lada da abubuwa na karamcci, akan haka ne ma Allah madaukakin sarki yake cewa:

﴿ مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗۖ وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٧ ﴾ النحل: ٩٧

**Ma'ana**: *"Dukkan wanda ya aikata na kwarai namijine ko mace yana mai Imani to hakika za mu rayar da shi rayuwa maikyau, kuma za mu sakanka musu dalansu da mafi kyawun abinda suka kasance suna yi"*. Suratun Nahl, aya ta:97.

Wadannan sune wani sashi na manufofin addinin musulunci, muna fata Allah Ubangiji ya tabbatar mana da ita mu da sauran al'ummar musulmi.

# Abubuwan dake ciki:

Gabatarwar mai fassara ....................................... 1

Addinin Musulunci ...............................................7

Rukunan musulunci ...........................................19

Tushen akidar musulunci .....................................27

Imani da Allah ...................................................30

Imani da mala'iku................................................70

Imani da littattafai ............................................82

Imani da Manzanni..............................................86

Imani da ranar karshe .......................................106

Imani da kaddara .............................................149

Manufofin akidar musulunci ...............................177

Abubuwan dake ciki...........................................184